KWATANTA KUMBURIN KALMA TSAKANIN HARSHEN HAUSA DA NA KAMUKU

NA

ABDULLAHI SHITU PANDOGARI

SPS/12/MHA/00009

BINCIKE DA AKA GABATAR A SASHEN KOYAR DA HARSUNAN NIJERIYA, JAMI'AR BAYERO, KANO.

DON CIKASA WANI VANGARE NA SAMUN DIGIRI

NA BIYU (M.A.) A HARSHEN HAUSA.

JANAIRU, 2017.

TABBATARWA

Ni Abdullahi Shitu Pandogari na tabbatar da cewa ni na gudanar da wannan aiki qarqashin jagorancin Farfesa M.A.Z Sani, kuma a iya sanina ba a gabatar da shi a wani wuri ba, haka kuma ba za a gabatar da shi a wani wurin na daban don samun digiri ba.

……...……..

ABDULLAHI SHITU PANDOGARI

SPS/12/MHA/00009

AMINCEWAR MAI KULA DA AIKI

Aikin wannan bincike wanda (ABDULLAHI SHITU PANDOGARI SPS/12/MHA/00009) ya gudanar, an yi shi ne bisa jagoranci na Farfesa M.A.Z Sani,

……

Farfesa M.A.Z Sani

Jagoran Wannan aiki

(Supervisor)

SHAFIN AMINCEWA

Ni Abdullahi Shitu Pandogari mai lamba SPS/12/MHA/00009 na gudanar da wannan bincike tare da amincewar ;

……

Farfesa U U Fagge

Mai duba aiki na Cikin Gida

(Internal Examinar)

……

Mai Duba Aiki na Waje

(External Examinar)

GODIYA

Godiya maras iyaka ta tabbata ga Maxaukakin Sarki Allah, wanda ya halicce mu kuma ya raya mu cikin qoshin lafiya, sannan ya zave mu daga cikin dubban jama'a, ya ba mu ikon yin karatu a wannan mataki, Allah mun gode. Sai yabo ga fiyayyen halitta Annabi Muhammad (SAW), wanda a dalilinsa ne muka kasance musulmi bisa turbar gaskiya. Allah ya qara masa daraja.

Iyayena, Malam Shitu Salihu (marigayi) da Malama Binta Ibrahim sun yi rawar-gani matuqa wajen tarbiyyantar da ni bisa turba ta ilimi, haka kuma gwaggo Asma'u da gwaggo Halima qarama da Halima babba duk sun yi ruwa da tsaki cikin abin da na zamo. Allah ya saka musu da 'Jannatul Firdausi' .

Yayata Habiba Shitu da qannaina Hadiza Shitu da Amina Shitu da Jibril Shitu (wanda Allah ya yi wa rasuwa 17/12/2012 Allah ya yi masa gafara) su ma sun taimaka sosai, na gode.

Farfesa Mu'azu Alhaji Sani Zariya, malamina, abin alfahari saboda ne irin gudummawar da ya yi ta ba ni tun lokacin da nake karatun digiri na farko, ba tare da gajiyawa ba. Haka

kuma ya kasance mai duba wannan aiki nawa, wanda ya yi ta sanya ni bisa hanya ba dare ba rana cikin farin-ciki da annashuwa. Allah ya saka masa da mafificin alhairinsa. Sai kuma Farfesa Usaini Usman Fagge mai duba aikina na cikin gida (internal examiner) wanda kuma shi ya duba aikina a digiri na farko, ya yi gyare-gyare da bayar da shawarwari, Allah ya saka masa da alhairinsa. Dukkan malaman sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero ta Kano, Allah ya saka musu da alhairi.

Abokan karatuna ma sun taka muhimmiyar rawa wajen ganin an sami nasarar kammala wannan aiki, kamar Malam Yakubu Ningi da Idris Gambo Kargi da Bashir Mahmud da Muhammad Fanti da Sulaiman Misau da Malama Hafsat Abdul'aziz Umar da Halima Haruna da ma sauran da ban ambaci sunayensu ba, haka kuma Buhari Aliyu na faculty of medicine Bayero University, Kano. Allah ya saka musu da alhairi.

Malam Abubakar Zukogi na sashen Ingilishi da Faransanci na Jami'ar Bayero, Kano shi ma ya taimaka matuqa wajen ganin

ci gaban harkokin karatu na sun kamala Allah ya saka masa da alhairi.

Malam Bala Adamu shugaban makarantar GSS Kamfanin Bobi da Abdullahi Mahanga da Mohammed Tanko da Akanga da Adamu Akayago Mohammed da Haruna Shekarau da sauransu, Kamukawa ne waxanda suka taimaka matuqa wajen sa ni a hanya game da abin da ya shafi harshen Kamuku, na gode matuqa.

Abokaina, irin su: Muhammad A Garba da Sanusi Abdullahi da Ado Sa'ad da Xayyabu Xahiru da Awwal Habib da Musa Mohammed Kwangoma da Yusuf Sa'ad Sai Buhari Aliyu da dai sauransu, sun qarfafa mani guiwa ainun, tare da ba ni dukkan goyon bayan da ya dace. Ina godiya a gare su baki xaya.

Maixakina malama Umma Habib, tare da 'ya'yana; Muhammad da Rahama da Rabi'at da Ibrahim da Jibril duk sun cancanci yabo bisa haquri da juriya da suka nuna ta fuskoki

daban-daban a lokacin wannan karatu nawa. Allah ya saka masu da mafificin alhairinsa, amin.

A taqaice dai, lokaci ba zai bari na ambaci sunayen kowa da kowa ba, don haka duk wani mai ruwa-da-tsaki da taimako kowane iri ne wajen ganin an sami nasarar kammaluwar wannan karatu nawa, ina matuqar godiya, Allah ya saka wa kowa da mafificin alhairinsa.

SADAUKARWA

Na sadaukar da wannan aiki ga mahaifana Malam Shitu Salihu da Malama Binta Ibrahim.

QUMSHIYA

Batu	Shafi
Shadin batu	i
Tabbatarwa	ii
Amincewar Mai Kula Da Aiki	iii
Shafin Amincewa	iv
Godiya	v
Sadaukarwa	ix
Tsakure	xv
Abstract	xvi

BABI NA XAYA

1.0 GABATARWA	**1**
1.1 Al'umar Hausawa	3

1.2 Al'umar Kamuku Da Harshensu 3

1.3 Alaqar Kamuku Da Hausawa 6

1. 4 Dalilan Bincike 8

1.5 Manufar Bincike 8

1.6 Muhimmancin Bincike 9

1.7 Farfajiyar Bincike 10

1.8 Tambayoyin Bincike 11

1.9 Hasashe 12

1.10 Kammalawa 12

BABI NA BIYU

2.0 Bitar Ayyukan Da Suka Gabata 13

2.1 Gabatarwa 13

2.2 Ayyukan Magabata 13

2.3 Kammalawa 30

BABI NA UKU

3.0 Hanyoyin gudanar Da Bincike 31

3.1 Hanyoyin Tattara Bayanai 32

3.2 Ra'in Da Aka yi Amfani Da Shi 35

3.2.1 Qirar Sarari Da Ta Voye A Harshen Hausa 36

3.2.2 Qirar Sarari Da Ta Voye A Harshen Kamuku 40

3.3 Yanayin Nazari 41

3.4 Kammalawa 42

BABI NA HUXU

4.0 Gabatarwa 43

4.1 Kumburi Jinsintarwa 44

4.2 Kumburin Samar Da Suna Na Asali 47

4.3 Jam'antawa 48

4.4. Jam'antawa A Harshen Kamuku 58

4.5 Bayanau Na Yanayi 66

4.6 Kammalawa 67

BABI NA BIYAR

5.0 Gabatarwa 68

5.1 Taqaitawa 68

5.2 Kammalawa 71

5.3 Shawarwari 72

MANAZARTA 74

RATAYE

Taswirar Yankuna Harsunan Nijeriya 80

Taswirar Yankunan Kamuku 81

TSAKURE

A wannan bincike mai taken Kwatanta kumburin kalma tsakanin harsshen Hausa da na Kamuku, an gano cewar harshen Hausa da na Kamuku sun yi tarayyar amfani da qwayar ma'ana ta /a/ don mayar da kalmomin tilo su koma jam'i, yayin da Hausa ke amfani da qwayar ma'ana ta /a/ xin a matsayin xafa-ciki da xafa-qeya, Kamuku kuwa na amfani da qwayar ma'ana ta /a/ xin ne a matsayin xafa-goshi don amfani iri xaya. Har wa yau kuma Hausa na amfani da qwayar ma'ana ta /a/ don jisintarwa, harshen Kamuku kuwa ba ya amfani da qwayar ma'ana ta /a/ wajen jinsintarwa.

Hausa da Kamuku sun yi tarayyar amfani da wata gava a matsayin xafa-goshi wajen samar da sunan mai harshe daga sunan harshe, ta wannan fuska, yayinda Hausa kan qara gava ta 'ba' a farkon sunan harshe don nuna mai harshen. Misali ; 'ba + gwari = bagwari', harshen Kamuku kuwa yana amfani da gavar 'bu' ne, misali; 'b + gwaar = bugwaar', wannan kenan yana nuni da yadda harsunan biyu suke amfani da gava makamanciya kuma a matsayin xafa-goshi amma da bambancin wasali a gavar da kowane ya yi amfani da shi.

Idan kuwa aka koma vangaren bambance-bambance, harshen Hausa na amfani da xafi iri uku (xafa-goshi da xafa-ciki da xafa-qeya) don kumbura kalma. Binciken da aka gudanar ya nuna cewar harshen Kamuku ba ya amfani da xafa-goshi don kumbura kalma. Haka kuma Hausa na amfani da xafa-qeya yayin jinsintarwa, harshen Kamuku kuwa na amfani ne da xafa-goshi wajen jinsintarwa kuma harsunan suna amfani da qwayoyin ma’ana mabambanta ne don jinsintawa.

ABSTRACT

In this research titled “Kwatanta kumburin kalma tsakanin harshen Hausa da na K amuku, it has been realized that both Hausa and Kamuku languages uses a common morpheme /a/ to make some of their singular words plural, while Hausa uses the /a/ morpheme as infix and suffix , Kamuku on the other hand uses the /a/ morpheme for but as prefix for the same purpose. Furthermore Hausa uses /a/ morpheme for another different purpose, that is in having feminine gender as in xalibi-xaliba. whereas is not so in Kamuku language. Again when it comes to the name of speaker of a language, Hausa adds syllable ‘ba’ as prefix to the name of the language for instance ‘ba + Gwari = Bagwari’. So also in Kamuku the syllable ‘bu’ also as prefix is added to the name of the language as in ‘bu + gwaar = bugwaar’. That is to say identical syllable is used even though with a difference in vowel. In terms of differences, while Hausa uses tree types of affixation (prefix, infix and suffix) to inflect words, from the research findings Kamuku doesn’t use infix in all its inflectional processes. In gender differentiations, Hausa uses infix and suffix for inflection, Kamuku on the other hand uses prefix for the same purpose.

BABI NA XAYA

1.0 Gabatarwa

Kwatanta tsakanin yanayin qirar kalma a harsuna mabambanta a fagen nazarin kimiyar harshe yakan qunshi qoqarin fitar da kamanni da bambance-bambancen da ake samu ne ta wannan fuska. A wannan bincike ma, kamar sauran, an yi qoqarinkamantawada kuma bambance tsarin kumburi tsakanin harshen Hausa da na Kamuku.

Sani (1999,2002 shf-89) ya bayyana kumburin kalma da:

838. “Kamar yadda anka faxa ma daxa,

Akwai `kumburi` nan wajen nazari.

839. A qirar fa kalma bayani nasa,

Yana nan tafe ai a wannan wuri.

840. Kalma tana kumbura dagga sai-,

Wa babu shakka akwai tabbaci.

841. Illa kawai wagga kalma ka san,

Ba sabuwa ba a wannan wuri.

842. Sabili da ko ai rukunni guda,

Take nahawu duk da wancan, ka ji.

843. Waccan da saiwarta tai sanadi,

Na samun fa wannan da munka gani.”

Kumburin kalma wani vangare ne na tasarifi wanda kan ja hankulan masu nazarin kimiyyar harshe saboda yadda yake da matuqar tasiri wajen qirar kalma a harsuna, domin kuwa nazarin kimiyyar harshe ya qunshiginshiqan vangarori guda huxu: (i) Tsarin sauti. (ii) Tasarifi/ qirar kalma. (iii) Ginin jumla. (iv)Ilimin ma’ana.

Masana, irin su Greenberg (1963) sun karkasa harsunan duniya kashi-kashi, wasunsu dangane da dangantaka ko nasabar furuci ko kusancin ma’ana, da dai sauransu. Manyan kashe-kashen su ne: Niger-Congo da Afro-Asiatic da Nilo-Saharan da Khoisan. Ga yadda Greenberg ya jeranta layin harsunan, wanda kuma harshen Kamuku ya shigo ciki: Niger- Congo, Atlantic-Congo, Benue-Congo, Kainji zuwa Kamuku.

1.1 Al' umar Hausawa

Hausawa mutane ne mazauna yankunan Arewacin Nijeriya da kuma kudancin Nijer har zuwa gavar tafkin Chadi, wato qasar Hausa a yau, kuma masu amfani da harshen Hausa a matsayin harshen uwa. Yaqe-yaqe, da farauta ko fatauci ko kasuwanci da neman ilimi gami da yaxa shi suna daga cikin dalilan da kan haifar da qaura, hakan ya haifar da kafuwar qasar Hausa, kuma suna daga cikin dalilan da suka sa Hausawa suka fantsama wurare da dama da suke zazzaune a yau. Jinju (1985) da Adamu (1997) da Kwakwaci, (2010).

1.2 Al'umar Kamuku Da Harshensu

Kamuku suna ne na wata qabila ko yare na wasu mutane da ke zaune a garuruwa irin su Pandogari da Kagara da Tagina da Mariga da Tungar-Baqo da Bobi da Kasuwar- Garba da Wamba da Galma da Sabonlayi da Gagumi da Uregi. Akwai kuma garuruwa irin su; Kungida Kuki da Kakangi da Randagi da Kubau da Kuyambanada Bugai da Kunungayya da Kurishi da Terebago, da dai sauran garuruwa waxanda suke cikin qananan hukumomin Rafi da Mariga na jihar Neja da kuma qaramar hukumar Birnin-Gwari ta jihar Kaduna a tarayyar Nijeriya.

Temple(1922 shf-205-14) ya nuna cewarKamuku suna zaune ne a yankunan gundumomin Kwangoma (Pandogari) yankin Naija zuwa Kotonkoro yankin gabashin gundumar Kontagora har zuwa gundumar Makangara, wasu kuma suna a yankunan qasar Kusheriki , akwai kuma wasu a yankin Teginada kuma a Birnin-gwari ta yammaciwaxanda aka qiyasta yawan su kimanin 34,500(dubu talatin da huxu da xari biyar) a wancan lokaci,(shf-205). Akwai ra'ayi mabambanta dangane da asalinsu; misali mazauna garin Kuki na iqirarin sun zo ne daga Zariatun kafin Jihadin Shehu Xanfodio, Su kuwa Kamukun Kakangi, Terebago, Kunungayya, Kabango da Kurishi na iqirarin asalinsu daga Kwatarkwashi ne, su kuwa 'yan kurigi suka ce su daga Kebbi ne , Kamukawan yankin Kwangoma kuwa sun ce asalinsu daga Katsina ne, da sauransu.

Shi kuwa Nakuta (1999shf30-45) ya bayyana cewa akwai karin harshen Kamuku kamar guda uku a duk farfajiyar Kamuku, su ne: Kamukanci (shi ne na ainihi), da Ura da kuma Acipanci. Ya kuma cigaba da bayyana asalin Kamukawa da cewa mazauna dutsen Makangara da Kusharki ne, kuma a wani qaulin ana danganta su da qabilar Samudawa. Akwai dai ra'ayoyi mabambanta dangane da asalinsu, wanda kuma Nakuta (1999) ya bayyana tun daga garuruwan da suke zaune.Misali, wasun su suna cewa asalinsu daga

Kwatarkwashi ne, wasu kuma sun ce Kabawa ne daga qasar Kabi. Su kuwaKamukawan Kwangwama, daga Katsina suke domin kuwa, in ji shi, suna da tsage (shasshawa) a kumatunsu, yawanci tsagen guda shida ko tara waxanda suke somawa daga mazaunin kunne zuwa kumatu (kundukuki) kamar dai na Katsinawa. Haka dai marubucin ya kawo misalai na al'adu da bukukuwa da camfe-camfensu da sauran xabi'un Kamukawa da garuruwansu.

Ta fuskar asalin yadda suka sami sunan yaren 'Kamuku' kuwa, Tsoho (2006 shf 1-3) ya tabbatar da cewa sunan Kamuku ya samo asali ne sakamakon haxuwarsu da Hausawa wato daga kalmomin Hausa 'Kamanku' inda ya qara da cewa sunan yaren kafin haxuwarsu da Hausawa shi ne 'Tu 'yara' kuma ya kawo maganar Bahaushen da ya zo yana koyar da yaransa karatu, akwai wani cikin yaran wanda yakan qi zuwa sai wani cikin Tu 'yara ya kawo shi ga Bahaushen sai ya ce ba ya son karatu 'Kamanku'. Haka kuma ya nuna cewar akwai ra'ayoyi biyu dangane da asalin Kamuku, ra'ayi na farko na cewa Kamuku sun fito ne daga gabas ta tsakiya sakamakon tsananin riqo da addinansu na gargajiya, da kuma tsananin qyamarsu da nuna adawa ga duk wani abinda ka iya tava ababen bautarsu, misali Kiristanci da addinin Musulunci,cikin tafiyarsu ne suka sauka Katsina da

musulunci ya shigo Katsina kuma sai suka qara gaba suka watsu zuwa wuraren da suke a yanzu. Xaya ra'ayin kuma na cewa harshen Tu 'yara mu'ujizace daga Allah don kuwa an ce wasu mutane ne mafarauta su uku waxanda suka sauka a wani gari Kuki, kuma ya kasance su ukun babu mai jin harshen xan'uwansa, kwatsam sai wata rana suka wayi gari suna yaren Tu 'yara, sai kawai suka cigaba da jin junansu.

1.3Alaqar Kamuku Da Hausawa

Kamuku ko Kamukawa mutane ne da tun lokaci mai tsawo suke zaune kan tsaunuka, Mashegu (2008 shf1-2) ya bayyana cewar a dalilin alaqar Kamuku da Hausawa ne aka sami sunan harshen Kamuku. Domin kuwa, in ji shi, kafin mu'amalarsu da Hausawa, masu wannan harshe ana kiran su da"*Gatu'yara"* da harshen na Kamuku wato gatu na nufin mutane, '*yara* kuma kibiya (mutanen kibiya). Hausawa ne suka zo suka zauna a garuruwan 'gatu 'yara' suna koya wa yaransu (Hausawan) karatu. Ana haka sai aka sami wani daga cikin yaran wanda yakan gudu zuwa wurin wasa tare da sauran yaran Tu'yara waxanda ba su karatu. Sai wata rana aka kawo qarar

wani daga cikin yaransa (Shi Bahaushen) mai qin ji wanda ya qi karatu. Bahaushen ya amsa masa da cewa ba ya son karatu ‘Kaman ku’. Daga wannan lokaci aka ci gaba da yi musu laqabi da ‘Kamanku’. Bayan xan lokaci, kalmar ta koma Kamuku har zuwa yau da ake amfani da ita a matsayin sunan harshen.

Shi ma Bobi (2008 1- 5) ya nuna cewarasalin sunan na Kamuku ya samu ne bayan haxuwarsu da Hausawa, kamar dai yadda sauran suka bayyana.

Haka kuma, a duk zantawar da kuma hirarrakin da aka gunar yayin wannan bincike, bayanan da aka samu sun bayyana cewa kalmar ‘Kamuku’dai ta samo asali ne daga faxar Bahaushe ‘kamanku’. Duk da cewa dai labaran nasu na kunne-ya-girmi-kaka ne, cewa suka yi Bahaushe ne ya tambayi wani ‘*Ga ‘yara’* cewa ku waxanne irin mutane ne? Sai aka amsa masa da ‘mu mutane ne ‘kamanku’ , sai ya ji kamar an ce ‘kamuku’. To, sai ya kasance idan za su yi maganar abin da ya shafi ‘*Ga ‘yara* ‘, sai su ce ‘kamuku’. Haka kuma, su ma sun qara tabbatar da cewa sunan harshen kafin haxuwarsu da Hausawa, shi ne, *‘Ga ‘yara*’, kamar dai yadda Mashegu ya bayyana a baya.

Kenan a iya cewa dangane da binciken da aka gudanar bayani ya zo xaya game da yadda aka samu sunan na Kamuku, wato dai daga Kalmomin Hausa na'kaman'da 'ku', amma a vangaren asalin Kamuku ne aka sami ra'ayoyi mabambanta, waxanda suka danganta da wurin zama ko yankin da Kamukun suke a zaune.

1.4 Dalilan Bincike

An qudurta gudanar da wannan bincike bisa dalilai kamar haka :

(i) Bayar da gudummowa ga fagen nazarin harshe

(ii) Qarancin bincike ko rubuce-rubuce a harshen Kamuku, musamman, idan aka ce za a kwatanta da nazarce-nazarce a harshen Hausa da aka daxe ana yi. Ba ma sai an gwada ba.

(iii) Qara zaburar da masu bincike don su faxaxa.

(iv) Sha'awar da mai bincike yake da shi a fannin nazarin kimiyyar harshe don qara faxaxa sani.

(v) Qarawa masu sha'awar bincike qwarin guiwa.

1.5 Manufar Bincike

Manufar wannan bincike, ita ce, kwatanta kumburin kalma tsakanin harshen Hausa da na Kamuku, don:

(i) Fito da wuraren da suka yi kamanceceniya ta fuskar amfani da qwayar ma’ana ko kuma wurin da kumburin yakan shafa.

(ii) Fito da wuraren da suka yi hannun riga ta wannan fuskar.

(ii) Share fage ga masu sha’awa don faxaxa bincike.

1.6 Muhimmancin Bincike

Kwatanta tsakanin wasu lamurra na harsuna mabambanta a fannin kimiyyar harshe muhimmi ne. Ba don haka ba kuwa, da masana kimiyyar harshe ba su iya fitar da wasu xabi’un da sukan zama ruwan dare ga harsunan halicci na xan Adam ba. Irin waxannan bincike-bincike suna taimakawa matuqa wajen samar da sahihiyar alqibla ga masu nazarin kimiyar harshe, inda hakan, yakan haifar da samar da wasu dokoki na bai xaya.

Masu sha’awar nazarin kimiyyar harshe ta vangaren tasarifi za su amfana ta fuskoki, kamar haka:

i. Havakawa da bunqasa harshen Hausa tare kuma da bayar da gudummawa ga nazarin harshen Kamuku, musamman.

ii. Fitar da ire-iren qwayoyin ma’ana masu haifar da kumburi a harshen Kamuku.

iii. Gano wurare da yanaye-yanayen da ake xafa qwayoyin ma’ana a kalma ta kumbura a harshen Kamuku.

iv. Fayyace kamanni da bambance-bambance na ire-iren qwayoyin ma’ana da yanaye-yanayensu ta yadda ake samun kumburi a harshen Kamuku.

v. Qara qwarin guiwa, gami da zaburarwa, ga masu sha’awar wannan fanni don faxaxa bincike.

vi. Zaqulo wasu lamurra na kumburi a harshen Kamuku, da kwatanta su a harshen Hausa, don gano inda suka haxu da inda suka yi hannun riga.

vii. Bayar da gudummowa gwargwadon iko ga nazarin tasarifin a harshen Hausa da na Kamuku.

1.7 Farfajiyar Bincike

Wannan bincike zai taqaita ne ga tsarin kumburi a qirar kalmomi kaxai, wani vangare na tasarifi. Bai shafi sauran hanyoyi na qirar kalma irin su: tsira da harxantawa ko ninki da sauransu ba, ballantana kuma uwa-uba

sauran ginshiqan vangarori na kimiyar harshe, irin su: tsarin sauti ko ginin jumla ko kuma ilimin ma'ana. Don haka aikin zai kalli yadda lamarin kumburi yake ne a harshen Hausa, ya kwatanta shi da yadda yake a harshen Kamuku, don rarrabe tsakanin zare da abawa. Ma'ana, a fitar da wuraren da suka yi kamanceceniya da kuma wuraren da suka yi hannun riga da juna.

1.8 Tambayoyin Bincike

A wannan bicike, za a yi qoqarin amsa waxannan tambayoyi:

i. Shin qwayoyin ma'ana iri xaya harshen Hausa da na Kamuku suke sarrafawa ta fuskar kumbura kalma?

ii. Ko akwai wata ko wasu kamanceceniya tsakanin harsunan biyu?

iii. Ko akwai wani ko wasu bambance-bambance tsakanin harsunan biyu ta fuskar yanayin amfani da qwayar ma'ana wajen kumbura kalma?

iv. Shin xafe-xafe don samar da kumburin kalma iri xaya ne a harsunan biyu .

1.9 Hasashe

Harshen Hausa da Kamuku suna amfani da xafin qwayar ma'ana wajen kumbura kalma. Tarayyar harsunan biyu kan amfani da wata ko wasu qwayoyin ma'ana don kumbura kalma. Sai samun qwayoyin ma'ana da kowane harshe ya kevanta da shi wajen kumbura kalma.

1.10 Kammalawa

A wannan babi, an bayyana ko su wane ne Hausawa a taqaice, haka kuma aka kawo ko su wane ne Kamuku (Kamukawa) da wuraren zamansu, da kuma alaqar da ke tsakaninsu da Hausawa. Haka kuma, aka zaqulo kamanni da bambance-bambancen tsarin kumburi a harsunan biyu. Sai ire-iren qwayoyin ma'ana tare da fayyace kamanceceniya da bambance-bambance, da aka samu a tsarin kumburi a harsunan biyu. Bugu da qari an hasaso yiwuwar samun kamanni da bambance-bambance a tsarin kumburi na harshen Hausa da na Kamuku, wanda binciken ya tantance.

BABI NA BIYU

2.0 BITAR AYYUKAN DA SUKA GABATA

2.1Gabatarwa

Masana da dama sun daxe suna qoqari a fannonin bincike da dama. Wannan aiki na ‘Kwatanta KumburinKalma Tsakanin Harshen Hausa da na Kamuku’, ya shafi wani vangare ne kaxai na tasarifi wato kumburi, domin fito da wuraren da harsunan biyu suke da kamanci da bambanci ta wannan fuskar.

2.2 Ayyukan Magabata

Yusuf (2010) ya bayyana ma’anar nazarin kimiyar harshe da “Dukkan bayanan nahawu waxanda ke bayani game da yanayin harshe ta fuskar sauti da kalmomi da yankin jumla da ma jumla, da dai sauransu.” Shi kuma Fagge (2012) ya bayyana nazarin kimiyar harshe ne da cewar nazarin harshe a kimiyance. A nan, a kimiyance yana nufin dogaro da dabaru da matakan bincike na kimiya da suka shafi kiyayewa da qwanqwancewa ta hanyar bincike kafin samar da sahihin ra`i, wanda kuma ita ce sahihiyar hanya a

nazarin kimiyar harshe, kamar dai yadda abin yake a sauran fannonin kimiyya.

Abubakar (2001) kuwa, ya bayyana ma`anar tasarifi ne da cewa nazari ne da ya qunshi samar da kalma da kuma kumburi. Bugu da qari,Fagge (2012shf 29) ma, ya bayyana ma`anar tasarifi da nazari na tsarin kalma.

Daga cikin hanyoyin da ake amfani da su wajen qirar kalma, akwai : kumburi, tsira da harxantawa da ninki da fassara da qirqira, da dai sauransu.

Ladan (1981shf 48 - 62) ya yi bayanai da suka shafi jam`antawa da kuma jinsintawa na Hausa, inda ya yi bayyani matuqa game da kumburi da tsira da ninki a matsayin ginshiqan hanyoyin qirar kalma.

Aikin Ladan ya shafi kumburi da tsira na harshen Hausa, shi kuwa wannan bincike namu zai kalli tsarin kumburi ne ta hanyar kwatanta shi a harshen Hausa da na Kamuku.

Lyons (1968) ya yi nuni ne da cewa ana samun kumburi ne daga saiwa ko saiwoyin kalma, wanda kuma duk tsarin na aukuwa ne a yanayi na tsarin ginin jumla, haka kuma duk kalmomin daga tushe xaya ne.

Shi kuwa Abubakar (2001) cewa ya yi, tsarin tasarifi na kumburi ya shafi tsare-tsaren kalmomi ba tare da canjin aji ba, ta yadda za su kasance a rukunin nahawu xaya. Misali kalmomin *yar-o* (namiji tilo) da *yar-inya* (tamata tilo) da *yar-a* (jam`i) dukkan su suna rukunin nahawu xaya ne wato suna, ko kalmomin *dog-o* (namiji tilo) da *dog-uwa* (tamata tilo) da *dog-aye* (jam`i) duk dai kalmomi ne na sifa;haka *harb-a da harb-e da harb-i da harb-o* da kuma *harb-u* duka aikatau ne, da dai sauransu.

Fagge (2012) ya nuna kumburi da cewa: tsari na tasarifi da akan qara xafe-xafe ga saiwar kalma a iyakance tasirinta a nahawunce don tantantace rawar da nahawu ke takawa, kamar a wajen samar da jinsi ko adadi. Misali:

Jinsi Na Hausa

Namiji	Xafin kumburi	Tamata
jà:ki:-aa	jà:kà:	
jibge:gè	-iya:jibgeg-ìya:	
za:k-ìi-anyà	za:k-anyà	
màra:yà:-niya	màrainìya	
Tso:ho:-uwa	tso:huwa:	

A kowane misali cikin misalan da suka gabata, saiwa ceta kalma xaya takan sami xafi inda take kumbura don jinsintarwa (daga namiji ta koma mace).

Idan kuma aka koma vangaren adadi wato abu xaya ya koma fiye da xaya ko a ce tilo da jam'i, nan ma akan sami kumburin saiwar Kalmar tilo don komawa jam'i ta hanyarqarin xafin qwayar ma'ana. Misali;

Adadi Na Hausa

Tilo	**Xafin kumburi**	**Jam`i**
ya:r-ò:	-aa	yâ:r-a:
marò:q-i:	-aa	marò:qa:
ma:y-è:	-uu	ma:y-u:
la:y-à:	-uu	la:y-u:
qwà:r-o:	-ii	qwà:r-i:
kà:z-a:	-ii	kà:j-i:

Fagge (2012) ma ya taimaka sosai wajen yin jagora da qarin haskega wannan bicike don tantance ko haka abin yake a harshen Kamuku.

Baalou (1997shf 31- 41) ya yi bayani dangane da yadda ake samun kumburi cikin wasu harxaxxun sunaye, waxanda kan haifar da samun kalmomin tilo su koma jam'i. Misali: Gida-n sauro-- gidajen sauro, Qudan zuma - qudajen zuma, Ke:ken do:ki- ke:kunan do:ki. Hular kwano - hulunan kwano. A nan, kumburin kan shafi kalmar sunan da ke zuwa ne a farko, ba tare da shafar xaya kalmar ta sunan ba. Amma kuma, hakan yakan shafi harxaxxen sunan da ya qunshi kalmomin sunaye biyu da mahaxi a tsakiya kaxai, ban da sauran harxaxxun sunaye masu saiwoyin da ba suna ba, kamar: rub-da-ciki, sha-ka-tafi, ka-fi-shanu-wuya, da sauransu masu qunshe da tushen da ba kalmar suna ba. Ya ci gaba da bayyana cewar kumburin na faruwa ne ga kalmomin da suke vangaren hagu na harxaxxun sunaye kaxai.Aikin na Baalou ya fitar da yanayin kumburi a harxaxxun kalmomi,sai dai aikin nasa ya sha bamban da wannan bincike, domin kuwa, ya karkata ne kan matakan tasarifi na harshen Hausa, wannan kuwa yanayin kumburi tsakanin harshen Hausa da na Kamuku yake kallo.

Baba (2006) ya kalli sautukan harshen Hausa da na Larabci, kama daga haxuwar sautukan da rarrabuwarsu har zuwa tsarin gava da tsayin wasali har da su nannage, da sauransu. Duk da cewa aikin Baba (2006) tsarin sauti ne, bai hana wannan bincike da ya shafi tasarifi fa'idantuwa da shi ba,

kasancewar kwatanta harsuna biyu aikin ya yi, kamar dai wannan aikin, sai dai kuma wannan da ake zance ya shafi harshen Hausa ne da na Kamuku.

Maikuxi (2008) ya kwatanta tsarin sifa a harshen Hausa da na Yarbanci, kamar inda ake amfani da sifa a yankin suna a harsunan biyu. Misali, Hausa: kalmomin *fari, baqi da sabo*, Yoruba: *fufu, dudu, tuntun,* da sauransu. Haka kuma, amfani da sifa a matsayin sifatan qeya. Misali, *'kare fari'; 'aje funfun'. 'akuya baqa'; 'ewure dudu'.* Harsunan biyu suna amfani da ninki na kalmomin sifa, kuma sifa kan iya zuwa a matsayin suna, da sauransu.

Akwai kuma wuraren da harsunan suka yi hannun riga, kamar yadda ake amfani da kalmomin sifa a sifatan goshi, inda hakan ba ya faruwa a harshen Yarbanci. Misali, Hausa: *'Farin kare'*, Yoruba: '**funfun aja', 'Farar akuya' , ' *dudu ewure'.*

Wannan aikin ya dubi wani vangare ne na ginin jumla, amma kuma an amfana da shi, ganin yadda ya shafi kwatance tsakanin harsuna guda biyu na Hausa da Yarbanci. Amma kuma wannan aikin da ake gabatarwa duba kumburin kalma a harsunan Hausa da na Kamuku yake yi.

Suleiman (2010) ya bayyana wuraren da qirar kalma a harshen Ebira da na Turanci suka yi kamanceceniya da kuma wuraren da suka bambanta.

Ya fara da tantance adadin haruffan harshen Ebira da na Turanci, ta hanyar fitar da wuraren da suka yi tarayya da kuma inda suka sha bamban. Haka kuma, tsarin jam`antawa ta hanyar nuna irin xafe-xafen da ake yin amfani da su wajen haka, da sauransu. Duk da dai aikin na Suleiman ya yi wa tasarifi kallon gandu ne, amma kuma ya shafi kwatantawa tsakanin harsuna biyu mabambanta. Kenan aikin nasa ya bambanta da wannan bincike, wanda ke kwatanta tsarin kumburin kalma tsakanin harshen Hausa da na Kamuku.

Shi kuwa Yusuf (2011) nazari ya yi kan abin da ya shafi kamanci da bambanci na tasarifin harshen Hausa da na Larabci. Ya fito da fitattun wuraren da harsunan suke yin amfani da qwayoyin ma`ana iri xaya don samar da kalmomi masu yanayin ma`ana xaya, wato dai ta fuskar kumburi. Misali:

HAUSA

Tushe	**Kumburarriyar kalma**	**Ingilishi**
Kanò	bàkan- ìya	Kano woman
Zàmfàrà	bàzamfar-ìya	Zamfara woman
Misra	bàmisr-ìya	Egyptian woman

Sù:dân bàsudan-ìya Sudanese woman

LARABCI

Tushe	**Kumburarriyar kalma**	**Ingilishi**
KanòKanaw-iyya ko tun		Kano woman
Hausà	Hausaw-iyya ko tun	Hausa woman
Misrà	Misr-iyya ko tun	Egyptian woman
Sudân	Sudan-iyya ko tun	Sudanese woman.

Haka kuma, akwai inda harsunan Hausa da na Larabci suka yi tarayya wajen amfani da qwayar ma`ana ta `

‘ma-‘ (Hausa) da ‘mi-‘ (Larabci) wajen nuna kayan aiki, kamar:

HAUSA		**INGILISHI**
Tushe	**Kumburarriyar kalma**	
Go:gè	mà- gò:gi:	rubber/cleaner

Girbì: mà-girbi: cutter/harvester

Burgà mà- burgi: stirrer.

LARABCI

Tushe	**Kumburarriyar kalma**	**Ingilishi**
Fataha	miftaah ko u	key
Nashara	minshar ko u	file
Sabaha	misbah ko u	lantern

Haka dai Yusuf (2011) ya yi ta fitar da wurare na amfani da xafi iri daban-daban cikin hikima da basira kuma ya tantance wuraren kamanci da bambance-bambance a harsunan biyu. Har batun ninkin kalma ma ya kawo. Aikin nasa ya shafi vangaren tasarifi ne da kuma kwatanta harsuna mabambanta, kamar wannan bincike da ake gudanarwa. Sai dai harsunan da abin ya shafa ba xaya ba ne, haka ma manufofin binciken sun bambanta.

Imam (2011 shf 42 - 53) bincike ya gudanar game da kamanni da bambance-bambance da ke akwai tsakanin harshen Hausa da na Larabci ta fuskar ire-iren qwayoyin ma’ana da yanaye-yanayen amfani da su wajen qirar kalma a harsunan biyu.

Turbar binciken da ta wanda ake gudanarwa, ita ce, kwatancin harsuna biyu mabambanta ta fuskar qirar kalma, sai dai kuma harsunan wancan bincike da na wanda ake gudanarwa yanzu sun sha bamban, kuma shi wannan binciken ya shafi kwatantawa ne ta fuskar kumburin kalma kaxai.

'Yar'aduwa (1982) ya dubi yadda kalmomin *ma'auni*ke kumbura, wanda shi ne babbar alaqarsa da wannan aiki da ake gudanarwa. Abin da ya bambanta shi da wannan aiki, shi ne, aikin ya kalli kumburi ne a wani rukuni xaya na nahawu, shi kuwa aikin yanzu yana kallon kumburi ne a rukunonin nahawu da dama tare da kwatanta su da yadda lamarin yake a harshen Kamuku.

Saleh (2014 shf 5-15) ya nazarci yadda tasarifi kan shiga cikin tsarin sauti ko tsarin sauti ya shiga tasarifi. Aikinsa ya shafi kwatanta wasu lamurra ne a harsuna mabambanta (wato Hausa da Bade), shi ko wannan bincike yana magana ne kan harshen Hausa da Kamuku ta fuskar kumburin kalma.

Newman (1967) da Mukoshy (1978) da Rufai (1985) da Zarruq (2002, 2004), duk sun yi tsokaci ne matuqa game da abin da ya shafi jam`antawa a Hausa. Dukkan waxannan ayyuka suna da matuqar tasiri ga

binciken da ake gudanarwa ganin yadda kumburi ya kasance wata muhimmiyar hanya ta jam`antawa a kalmomin Hausa,wanda kuma yake cikin abubuwan da shi wannan aiki zai kalla ta hanyar kwatantawa da yadda lamarin yake a harshen Kamuku.

Halima (2011 shf 52-79) ta gudanar da bincike ne kacokan game da kumburin kalmomi a harshen Hausa inda ta fitar da qwayoyin ma'anar da kan haifar da jam'antawa da jinsintarwa, har ma ta kalli wasu azuzuwan kalmomi irin su sifa da aikatau da 'yar mallaka (gajeruwa -n ,-r ,-n), da bayanau da wakilin suna da madanganci inda ta nuna yadda kumburi kan shafe su. Misali: mallaka –n, -r,-n ; madanganci -n,-r,-n. sifa ; dolo-dolaye, gantalalle-gantalallu, xan –fari, 'yar-fara, aikatau; gama-gamo-game-gamu, karva-karvo-karve-karvu, yanka-yayyanka zuba-zuzzuba. Bayanau; safe-sassafe, asuba-asussuba, yagee-yayyage, karye-kakkarye kusa-kurkusa, da sauransu. Aikin yana da alaqa ta qut-da-qut da wannan ganin cewa batun ya shafi kumburin kalma ne. Sai dai wannan aikin ba kumburi a harshen Hausa kaxai ya tsaya ba kamar nata, ya ma haxa da na Kamuku.

Maryam (2007 shf 23-28) nazari ta yi kan kamanci da bambanci da ke tsakanin Hausa da Turancin Ingilishi ta fuskar jinsi, inda ta kalli yadda

harsunan biyu suke amfani da xafa-qeya a kumburin samar da jinsintawa. Misali;

HAUSA	ENGLISH
mawà:qi- mawa:qìya:	poet-poetess
qa:tò:-qa:tùwa:	giant-giantess
tura:rò-taura:rùwa:	actor-actress
ja:rùmi:-ja:rùma:	hero-heroien.

Ta bayyana yanayin lamuni, wato wuraren da bambancin kalmar tamata da namiji ba su da nasaba balle asali na kasancewa daga tushe ko saiwa xaya, Misali;

HAUSA	**ENGLISH**
xa:-'ya:	son- daughter
zàkarà-kà:za:	cock-hen

Haka bayanai suka tafi… da dai sauran hanyoyin jinsintarwa, waxanda kumburi kan shafa. Wannan ne ke nuni da dangantakar aikin nata da wannan aiki, domin kuwa, kumburi wata muhimmiyar hanya ce ta samar

da jinsintarwa a kalmomin Hausa, amma wannan aiki ya sa gabansa ne kan kwatanta kumburi a harsuna biyu mabambanta.

Gambo (2009) kwatance ya yi tsakanin harshen Hausa da na Turancin Ingilishi ta fuskar amfani da xafi a qirar kalma. Ya kawo xafin kumbura kamar: -a,-e,-i, -ai,-aye,-anu,-ka,-una,-uwa, da sauransu. Ya kawo Zarruq (1999) da ya yi maganar motsa kalma daga tilo zuwa jam'i 'xan-'yan, ko-an' don samar da kumburin wasu kalmomin sifatau da manuniya da na dogarau da tambaya, da sauransu wajen mayar da kalmomin tilo su koma jam'i, kamar ; wannan-waxannan, wancan-waxancan, wanda-waxanda, wane?-waxanne?, kowane- kowaxanne. Haka kuma ya kawo aikin Abubakar (2001), gurgu-guragu, kurtu-kurata, garma-garemani, garwa-garewani da sauransu. An tasirantu matuqa da wannan aikin, kuma aikin duk da cewa ya bambanta da wanda ake gudanarwa, domin kuwa mabambantan harsuna ayyukan biyu suke kwatantawa.

Kwatancin qirar kalmar Hausa da ta Badanci shi ne abin da Musa (2014) ya kalla, inda ya fara tun daga ire-iren qwayoyin ma'ana da harsunan biyu suke amfani da su a tsira da kumburin kalma da kuma harxantawa da ninki. Duk ya kawo su ya kwatanta na harsunan biyu, ta hanyar bayyana wuraren

da suke da kamanci da wuraren da suka bambanta. Aikin ya shafi kwatanci tsakanin harsuna biyu kamar wanda ake gudanarwa, sai dai harsuna ne mabambanta.

Mukoshy (1984) nazari ya yi game da tsarin sauti da qwayoyin ma'ana na harshen Fulfulde, sannan ya fitar da wuraren da wasu harsuna irin su Hausa da Larabci suka yi tasiri kan tsarin sauti da tasarifin Fulfulde. Nazarin nasa ya shafi harsuna biyu ne, wanda kuma shi ne alaqarsa da wannan bincike da ake gudanarwa.

Busa (2012 shf 25-78) kwatanci ya yi kan tsarin sautin harshen Hausa da na Gbagyi, wanda harshe ne na maqwabtan Kamukawa, a jihar Naija, kuma ma jama'arabokan wasan juna ne. Duk da cewa ya qunshi harsuna mabambanta kamar irin na aikin da ake gudanarwa, batun ma ba xaya ba ne, haka ma harsunan da kwatancin ya shafa suna da bambanci.

A wannan gava, ya zama tilas a duba rubuce-rubuce na harshen Kamuku, duk da cewa ba wani yawa gare su ba.

Kure (2014 shf 1-3) ya kalli hanyoyin sasantawa ne na gargajiya, a Masarautar Kagara, qaramar hukumar Rafi ta jihar Naija (wani yanki da Kamuku ke zaune). Alaqar wannan aiki da binciken da ake gudanarwa ta

nesa ce, domin kuwa, batun bai shafi aikin ba, sai dai mai wancan binciken ya tavo batun harshen Kamuku da kuma wasu yankunan da jama’ar suke zaune.

Mashegu (2008 shf 11-15) ya kawo tsarin qirga a harshen Kamuku sannan a qarshe ya kawo ire-iren xafin da kan haifar da jam`antawa a harshen na Kamuku. Kamuku kan samar da kalmomin jam’i ta hanyar amfani da xafa-goshi da musayar gurbi na wasali… Galibi xafe-xafen kan gabaci qwayar ma’ana da ke kasancewa saiwa. Mashegu (2008) ya yi qoqarin bayyana yadda tsarin jam`antawa yake a harshen Kamuku ta hanyar nuna qwayoyin ma’anar da akan xafa, kuma akan xafa qwayar ma`anar ne a farkon saiwar kalma. Qwayoyin ma`anar da ake amfani da su sun haxa da: ‘*she-*‘ da ‘*sha-*‘ da ‘*mo-*‘ da kuma ‘*mu-*‘ Misali;

KAMUKU		**HAUSA**	
Tilo	**Qwayar ma’ana**	**Jam`i**	**Tilo-Jam’i**
àma:ci	she-	she-ma:ci	tsohuwa-tsofaffi
àna:ta	she-	she-na:ta	gizogizo-gizogizo

a:wàsha-		sha:-wàkare-karnuka	
à:màh	sha-	sha:-màh	biri-birai
e:no:no	mo-	mo-no:no	tsuntsu-tsuntsaye
eyra	mo-	mo:- eyra	kibiya-kibiyoyi
e:shè	mo-	mo-e:she	ido-idanuwa
ima:ma	mu-	mu-ma:ma	tukunya-tukwane
itu:tu	mu-	mu-tu:tu	jaka-jakkuna.

Akwai inda ake jam`anta kalma ta hanyar musanya wasalin farko, kuma a matsayin xafa-goshi. Misali :

KAMUKU		**HAUSA**		
Tilo	***Musayar wasali***	***Jam`i***	***Tilo***	***Jam`i***
u:hi	u-a	a:-hi	kai	kawuna
o:nono	u-o	a:-nono	aku	aku

Wannan tsarin ya yi kama da wani tsarin jam`antawa na Hausa, inda ake samun musayar wasalin qarshe kurum don mayar da tilo zuwa jam`i, kamar

a kalmomi irin su *yaro-yara* da *maroqi- maroqa*, maye-mayu da *qwaro-qwari* a matsayin xafa-qeya savanin na Kamuku xafa-goshi da sauransu. Mashegu (2008) ya kalli qirga da jam`antawa ne kawai, wannan aiki kuwa zai kwatanta tsarin kumburin kalma ne a harsunan biyu, Hausa da Kamuku.

Shi kuwa Pandogari (1990) a kundin digirinsa na farko, ya yi nazarine game da yadda tsarin mulkin Kamukawa yake da kuma tasirin sarakunan gargajiya a tsakanin shekarun 1900 zuwa 1988, inda a ciki ya nuna yadda yanayin qasar Kamuku take da kuma garuruwansu. Sai kumabayanin da ya yi da ke nuna cewar kafin qirqiro jihar Naija a shekarar 1976 ana kiran yankin da 'KAMUKU NATIVE AUTHORITY' don inji shi skwai wasu harsuna a yankin amma Kamuku su ne suke da rinjaye. Shi ma ya kawo batun asalin Kamuku cewa daga Gabas ta tsakiya suka yiwo hijira. Kuma ya bayyana Kamuku da mutane ne manema kuma mahalba, sannan a qarshe ya bayyana yanayin tsarin gudanar da mulki a qasar Kamuku. Wannan bincike ma ya taimaka sosai ga aikin binciken da ake gudanarwa, don kuwa ya yi qarin haske wajen qara sanin ko su wane ne Kamuku, wanda shi ne harshen dawannan binciken ke kwatanta tsarin kumburi na harshen Hausa da na Kamuku.

2.3Kammalawa

A wannan babi, an yi qoqarin bitar ayyukan da masu nazari suka gudanar a matakai daban-daban, duk da cewa ba a sami rubuce- rubuce a harshen Kamuku sosai ba, sai dai kuma, sandar da ke hannunka da ita kake kai duka. Saboda haka, an kalato waxanda aka samu, ya zuwa lokacin tattara waxannan bayanai.

BABI NA UKU

3.0 HANYOYIN GUDANAR DA BINCIKE

A babi na biyu, an kawo bayanai waxanda aka samo daga wasu ayyuka da suka gabata masu alaqa ta kusa da ta nesa da wannan bincike. Wannan babin kuma zai yi bayani ne game da hanyoyin gudanar da wannan bincike.

Tsarin kumburi wani vangare ne na tasarifi da ya shafi kumburin kalma a harshe. Kumburi reshe ne na kimiyyar harshe da ya shafi xafe-xafen qwayoyin ma'ana wajen samar da kalmomi na rukunin nahawu xaya. Wannan bincike ya ta'allaka ne da kwatanci tsakanin tsarin kumburi na harshen Hausa da na Kamuku, inda za a lura da ire-iren xafin da ake amfani da su a saiwar kalma domin kumbura ta a harshen Hausa da na Kamuku.

Saboda haka, an ziyarci gidan adana tarihi da kuma sauran wuraren da ya kamata masu nasaba ko alaqa da binciken, kamar xakunan karatu da gidajen mutane da ofisoshi, da sauransu, kuma an sami abubuwa da aka fa`idantu da su.

An yi amfani da hanyoyi da dabaru iri-iri yayin tattara bayanai don tantance xafi na kumburi, musamman dabarar nan ta sauraron zantuka cikin

natsuwa da lura, kasancewar harshe wani abu ne da ya jivanci furuci na suatuka, waxanda ake iya sauraro ganin cewa tsarin bayanin harshe ake amfani da shi ba na nazari na qirqirar harshe ba.

Da yake binciken ya shafi harshen Hausa ne da na Kamuku, an ziyarci garuruwan Kamuku, irn su: Uragi, Tungar Baqo, Tegina, Kungi, Kakangi da Pandogari da Kagara da Tagina da Mariga da Tungar-Baqo da Bobi da Kasuwar- Garba da Wamba da Galma da Sabonlayi da Gagumi da Uregi. Akwai kuma garuruwa irin su; Kungi da Kuki da Kakangi da Randagi da Kubau da Kuyambanada Bugai da Kunungayya da Kurishi da Terebago, don tattaunawa da su ta hanyar tambayoyin bincike da hira inda aka sami qarin haske da fatawa.

3.1 Hanyoyin Tattara Bayanai

Duk wani bincike da ake gudanarwa yana da matuqar tasiri wajen tantance nau'in dabarar da ta fi dacewa a yi amfani da ita don yin nasarar samun bayanai da tattara su, don cim ma manufa. Akwai hanyoyi da dama da aka bi don samowa da tattara bayanai. Ginshiqai daga ciki, su ne: gwaji da lura, akwai kuma sauraron zantukan harshen Hausa da na Kamuku, sai naxar jawabai a rikoda yayin hira da waxanda abin ya shafa, ga kuma

tambayoyin bincike, da sauransu. Amma kuma waxanda aka fi yin amfani da su kuma suke da matuqar tasiri ga wannan bincike su ne hira da tattaunawa da kuma bitar rubutattaun ayyukan da aka yi a baya.

Tattaunawa da hirarraki da aka gudanar don tattara bayanai sun qunshi sauraron zantuka da aka gudanar bisa xabi'a ta halitta wato, zantukan da aka yi ba tare da sanin cewa akwai wani da yake sauraro da wata manufa ba, inda aka sami bayanai daga zantuka lokacin da ake gudanar da harkoki na yau da kullum. A irin wannan yanayi, binciken ya fa'idantu da wasu muhimman bayanai waxanda aka samu daga zantukan mutane mabambanta inda aka fitar da kalmomi daga rukunonin nahawu daban-daban, ta yadda ba wai an tambayi wanda abin ya shafa ba ne, a'a, kawai dai zantuka ne na yau da kullum, sai aka yi la'akari da wuraren da aka sami kumburin kalma cikin bayanan, kamar dai yadda mai magana ya yi amfani da su ba tare da sanin cewa ana lura da kalamansa ba.. Haka kuma an tatttara bayanai ta hanyar hira da tambayoyi kai tsaye, yayin da aka rubuta kalmomi masu nasaba da binciken da ake gudanarwa. Wannan na nufin yayin wannan nazari an ba da cikakkiyar dama ba tare da karkata ga ra'ayi ko son zuciya ba, ta yadda hakan zai yi tasiri ga binciken da ake gudanarwa ba. Akan yi amanna da irin wannan tsari don samun bayanai dalla-dalla waxanda kan taimaka wajen

tantance dacewa ko akasin haka. An kwatanta bin wannan tsari matuqa, kuma aka yi amfani da shi wurin tattara bayanai tare da kwatanta su, inda a qarshe aka sami nasarar fitar da kamanci da bambanci, kamar yadda aka qudurta.

An tatauna da kimanin mutane casa'in waxanda suke daga shekaru goma sha biyu zuwa saba'in, kuma maza ne da mata, batare da la'akari da matayin ilminsu ba a wuraren da aka ziyarta.

Haka kuma, yayin gudanar da binciken an duba bugaggun littattafai da kundayen bincike daga jami'o'i da kwalejoji da sauransu don samun abubuwan da suke da alaqa da wannan bincike. Haka kuma an yi la'akari da abubuwan da ake bukata tare da kyawawan mu'amala da waxanda aka yi hulxar da su, yayin da ake tattara bayanan, wanda hakan ya taimaka qwarai, ga xorewar kyakkyawar dangantaka tsakanin mai bincike da waxanda aka yi mu'amala da su yayin gudanar da binciken.

Har wa yau kuma an yi amfani da rubutattun abubuwa, irin su bugaggun takardu na laccocin masana, zuwa takardun da aka gabatar a tarurrukan qara wa juna sani, damuqalu da jaridu, da dai sauransu, waxanda suka bayar da dama ta samun sauqin kwatanci tsakanin tsarin kumburin kalma a harshen Hausa da na Kamuku.

Da yake binciken ya shafi harshen Hausa ne da na Kamuku, kuma harshen Kamuku ya kasance harshe na biyu ne ga mai bincike, sai aka xauki wasu mutane biyu Kamukawa (masu amfani da harshen Kamuku a matsayin harshen-uwa) waxanda suka taimaka matuqa wajen tattara bayanai da tace su.

Baya ga su kuma, sai ‘yan kabukabu waxanda suka yi ta kai mu wurare ko garuruwan Kamukawa, kasancewar mafi yawan hanyoyin zuwa garuruwan da Kamukawan ke zaune ba su da kyau sosai.

3.2 Ra’in Da Aka Yi Amfani Da Shi

Da yake aikin ‘Kwatanta Kumburin Kalma Tsakanin Harshen Hausa da Kamuku’ ya shafi qirar kalma ne, an zavi yin amfani da ra’in nan na ‘Nahawun Tsira mai Sassauyawa’ (Transformational Generative Grammar, TGG) na Chomsky (1957),kamar yadda Lamidi (2008) ya kawo bayani gameda yadda aka samar da ra’in da kuma yadda aka yi ta samun gyare-gyare na (ST, EST,GB, ds), domin kuwa ra’in yana xauke da bayanin abin da ya shafi ginshiqan abubuwa uku (i) Abubuwan da tsarin jumla kan qunsa (phrase structure component) irin su , yankin suna da yankin aiki ko yankin bayani da sauransu. Sai (ii) Abubuwan da kan haifar da sauye-sauye (Transfomational component) wanda kan shafi

tsarmawa ko shafewa ko canjin gurbi, dasauransu. (iii) Sarrafa qwayoyin ma'ana ko qwayoyin sauti wajen qirar kalma (morphpphonemic/transformational component). Wani sashi na tasarifi mai qunshe da qirar voye da qirar sarari na kalma, wanda kuma shi ne qashin-bayan samar da kumburin kalmomi a harsuna. Hakan kuma ya shafi tsarin kumburi a harshen Hausa da na Kamuku.

3.2.1Qirar Sarari Da Ta Voye A Harshen Hausa

Idan aka ce qirar voye, ana magana ne game da yadda ake samun xafin qwayar ma'ana kai tsaye ga jikin saiwar kalma ba tare da wasu dokokin harshe sun yi tasiri ba, wanda kuma mafi yawa yakan sava da yadda ake amfani da shi a harshen halitta. Qirar sarari kuwa na nuni ne da yadda masu harshe suke amfani da harshen ko a ce yadda ake furuci ko lafazin kalma bayan duk wata doka ta qirar kalma ta gama aiki don samar da kumburi.

Daga cikin dokokin da kan shafi qwayoyin ma'ana yayin kumburi don samar da jam'i a harshen Hausa akwai:

(i) Ganxantawa

(ii) Kore ganxantawa

(iii) Kore levantawa da sauransu

Sani (2005 shf 33-39) ya bayyana yadda dokoki na (i), (ii) da (iii) na sama suke faruwa a Hausa. misali,

(i) Ganxantawa wajen samar da jam'i

Ganxantawa na nufin qara furucin ganxa ga baqin da ba baganxe ba bisa wasu sharuxxa. Wannan aiki ya duba ganxantawar da ke samar da jam'i, misali, kalmar Hausa ta bawa mai jam'i bayi. Ga yadda abin ya kasance :

/ba:wa:/	+ /-i:/	(xafin jam'i)
ba:wa:i:		(qirar voye)
ba:wi:		(shafe wasali)
ba:yi:		(ganxantawa)
[ba:ji:]		(qirar sarari/ lafazi)

Wato idan da dokar ganxantawa ba ta yi aiki ga kalmar bawa ba, da jam'inta ya kasance *ba:wi: , alhali kuwa ba haka lafazin yake a Hausa ba. Maganar qirar voye da ta sarari kenan.

(ii) Kore ganxantawa wajen samar da jam'i

Kore ganxantawa akasin ganxantawa ne, a nan kalma ce mai xauke da baqi xanganxa amma in aka mayar da kalmar tilo ta koma jam'i sai furucin na ganxa ya vace. Misali, kalmar Hausa ta alhaji mai jam'i alhazai :

/àlhajì:/ + /-ai/ (xafin jam'i)

àlhàji:ai (qirar voye)

àlhàjai (shafe wasali)

àlhàzai (kore ganxantawa)

[àlhàzai] (qirar sarari/ lafazi)

Dokar kore ganxantawa ce ta yi aiki inda lafazin [j] ya koma [z]. Nan ma misali ne na qirar voye da qirar sarari sun yi aiki.

(iii) Kore levantawa wajen samar da jam'i

Levantawa na nufin qara wa furucin baqi da ba baleve ba, kewayar levva. A wannan aiki kore levantawa na nufin baqin da a tilonsa yake da kewayar levva amma ya rasa wannan kewayar ta levva yayin komawarsa jam'i, misali a kalmar, kadarko mai jam'i kadarkai.

[kadark^{w}o:] + {-ai) (xafin jam'i)

kadark^{w}o:ai (qirar voye)

kadark^{w}ai (shafe wasali)

kàdàrkai (qirar sarari/ lafazi)

Akwai kuma irin su dolo-dolaye

/Do:lo:/ + /-à:ye:/ (xafin jam'i)

Do:lo:à:ye: (qirar voye)

Do:là:ye: (shafe wasali)

[Do:là:ye:] (qirar sarari/ lafazi)

Yayinda waxannan dokoki ke aiki (lokacin kumburi) in har saiwar kalmar ta qare da wasali, sannan kuma qwayar ma'anar da za a liqa ta kasance farkonta wasali ne, to sai wasalin da aka taras ya tashi ya bai wa wasalin da ya zo wuri.

3.2.2 Qirar Voye Da Ta Sarari A Harshen Kamuku

Misali na qirar sarari da na voye a wasu kalmomi a harshen Kamuku, kamar fartanya-fartanyu da Kamuku ake ce wa‘*i:’ob’* mai jam’i‘*mu’ob’*

/i:’ob/	+ /mu-/	(xafin jam;i)
mu’i:’o:b		(qirar voye)
mu’o:b		(shafe wasali)
[*mu’o:b]*		(qirar sarari/lafazi)

wuri-wurare, Kamuku su ce *à;hug* mai jam’i shìhu:g

/*àhu:g/*	+ /shi-/	(xafin jam’i)
shiahu:g		(qirar xoye)
shihu:g		(shafe wasali)
[shìhu:g]		(qirar sarari/lafazi)

varawo-varayi, Kamuku su ce *buzumb* mai jam’i *azumb*

/buzumb/	+ /a-/	(xafin jam’i)
abuzumb		(qirar voye)

azumb (shafe gava)

[*àzumb]* (qirar sarari/lafazi)

Ra'in Nahawun Tsira mai Sassauyawa (Transfomational Generative Grammar) mai qunshe da qirar voye da qirar sarari shi ne ya dace da wannan aikin, ganin yadda kusan duka tsarin kumburin waxanda akan samu a harsunan Hausa da Kamuku, sun shafi qirar sarari da qirar voye.

3.3 Yanayin Nazari

A wannan bincike, an dubi qwayoyin ma'ana ta fuskar wasu rukunonin nahawu kamar: suna da aikatau da sifa da bayanau da nunau da sauransu, da nufin gano ire-iren xafin da ake yi musu su kumbura.

Saboda haka a wannan bincike, an xauki salo irin na bayyana kowane rukuni na nahawu da ya shafi binciken ta fuskoki kamar haka;

(a) Bayyana ma'ana da kalmomin rukunonin nahawu da suka shafi aikin, tare kuma da karkasa qwayoyin ma'anar da ke haifar da kumburi a Hausa, sannan a kwatanta yadda lamarin yake a harshen Kamuku.

(b) Tsamo fitattun qwayoyin ma’na masu haifar da kumburi na kowane rukunin nahawu da aikin ya shafa, ta hanyar kawo misalai daga harshen Hausa, sannan a kwatanta da harshen Kamuku.

(c) Nuna sakamakon da binciken ya gano tare da tattara bayanan da aka samu kuma aka tace su ta yadda aka fitar da muhimman batutuwan da suka shafi wannan bincike, aka bayyana su ta hanyar kwatanta su da yadda tsarin yake a harshen Hausa da na Kamuku.

3.4 Kammalawa

Wannan babi ya yi wa hanyoyin gudanar da bincike kallon gandu ta yadda aka fara tun daga tuntuvar masana zuwa ziyarce-ziyarce da tattara bayanai da kuma tsara su don rarrabewa tsakanin zare da abawa yadda za a sami nasarar aiwatar da shi (binciken).

BABI NA HUXU

QALAILAICE BINCIKE

4.0Gabatarwa

Kamar yadda muka ambata a baya a shafi na huxu, Hausawa mutane ne mazauna yankunan Arewacin Nijeriya da kuma kudancin Nijer har zuwa gavar tafkin Chadi, wato qasar Hausa a yau, kuma masu amfani da harshen Hausa a matsayin harshen uwa. Yaqe-yaqe, da farauta ko fatauci ko kasuwanci da neman ilimi gami da yaxa shi suna daga cikin dalilan da kan haifar da qaura, hakan ya haifar da kafuwar qasar Hausa, kuma suna daga cikin dalilan da suka sa Hausawa suka fantsama wurare da dama da suke zazzaune a yau… Jinju (1985) da Adamu (1997) da Kwakwaci, (2010).

Kamuku kuwa suna ne na wata qabila ko yare na wasu mutane da ke zaune a garuruwa kamar Birnin-Gwari da Randagi da Pandogari da Kagara da Uregi da Mariga da sauran garuruwa na qananan hukumomin Rafi da Mariga da Bangi a jihar Niger da kuma yankunan qaramar hukumar Birrrnin-Gwari a jihar Kaduna, Nijeriya. Sunan wannan qabila ko yare ya samo asali ne sakamakon haxuwarsu da Hausawa, wani Bahaushe ne ya tambaya ko su waxanne irin mutane ne? Sai wani ya amsa masa cewa, mu mutane ne ‘kamanku’, daga faxarsu “KAMANKU”, wajen qoqarin faxar kamar ku sai Bahaushe ya ji kamar sun ce

Kamuku, don haka sai aka cigaba da kiran su hakan. Domin kuwa kafin haxuwarsu da Hausawa ana kiran su " GA EYRA"…. Nakuta (1999) da Mashegu (2008) da Akanga (2014) da sauranm waxanda aka tattauna da su.

Wannan binckeya kalli xafe-xafe ne da ake samu don kalma ta kumbura sakamakon xafin qwayar ma'ana a harsunan Hausa da na Kamuku.

4.1 Kumburin Jinsintarwa

Jinsi wani muhimmin sashi ne na nahawu da ya shafi azuzuwan kalmomi irin su suna da wakilin suna da sifa. Haka kuma, a tasarifin Hausa, akwai jinsi iri uku: namiji da mace da jinsin haxaka. Wannan aiki zai kalli kumburi ne da ake samu a kalmomi masu saiwa xaya tsakanin namiji da mace. Don haka binciken ba zai shafi tsarin jinsi na lamuni (jinga) ba, kamar: bùnsuru: – àkuya:, ra:go: – tunkìya:, angò: – amarya:, bùdurwa: – sauràyi:, gafiyà: – burgu:, do:kì: – go:x ìya:, zàkarà – kà:za:, mà:ge – mùzu:ru:. Haka kuma, ba za a kula da kalmomin da ba su da bambanci tsakanin namiji da mace ba, irin su: agò:là, kà:ka:, lauyà, da sauransu.

Jinju (1981) da Fagge (1993, 2004) da Abubakar (2001) da saoransu, sun yi bayanin kumburi don jinsintarwa inda suka fitar da qwayoyin ma'ana da jinsintarwa ta jivanta a harshen Hausa, kamar a waxannan misalai:

Qwayar ma'ana ta *–iya.* Misali, àbo:ki: – àbo:kìya:, kàwa:li: – kàwa:liya:, àmi:nì: – àmi:nìya:, àmìntacce: – àmintacciya:, rà:mamme: – rà:mammiya:, gabje:jè: – gabje:jìya:, xanxashe:shè: – xanxashe:shìya:, Bàhaushè: – Bahaushìya:, Bàyarbè:- Bayarbiya:, masò:yi: – maso:yìya:, ma'àikàci: – ma'àikacìya:, marùbuù:ci: – marubu:cìya:, mì:tsi:tsì – mì:tsi:tsìya:, sì:ri:rii: - sì:ri:riya:, da sauransu.

Qwayar ma'ana ta *–uwa*. Misali, qa:tò: – qa:tùwa:, bà:qo: – bà:quwa:, do:go: – do:guwa:, sa:bo: – sa:buwa:, tàura:rò: – tàura:rùwa:, da sauransu.

Qwayar ma'ana ta *–aa.* Misali: àlma:jìri: – àlma:jìra:, àljani: – àljana:, jà:ki: – jà:ka:, rùvavve: – rùvavva:, rà:yayye: – rà:yayya:, jamì'i: – ja:mì'a:, qàrami: – qàrama:, ka:fìri: – ka:fìra:, ja:rùmi: – ja:rùma:, gàje:re: – gàje:ra:,baqi: – baqa:, fari: – fara:, da sauransu.

Qwayar ma'ana ta – *anya :* za:kì: – za:kanyà:, birì: – biranyà:, da sauransu.

Qwayar ma'ana ta –niya. Misali : sâ: - sa:nìya:, màka:hò: – màkaunìya:, vra:wò: – vàraunìya:, màra:yaà: – màrainìya:, da sauransu.

Dangane da kumburi, wajen samar da jinsi a harshen Kamuku, binciken ya nuna cewa, da yawa daga cikin tsarin jinsintarwa(In har akwai) yana ta'allaqa ne ga qwayar ma'ana ta '*bùga:'*.- *da*'*bo'o:-'* . Bùga: na nufin namiji, bo'o: kuma mace, waxanda akan liqa a matsayin xafa-goshi ga saiwar kalma don ta kumbura ta jinsintar. Misali: kalmar harshen Kamuku t*a 'tuwa:g'*mainufin kwartanci, idan ana maganar kwarto namiji ne, sai a yi wa saiwar kalmar xafin qwayar ma'ana xafa-goshi ta 'buga:bò: '. A nan *bugaa-na nufin namiji, ' -bo-' kuma mai yi, ita kuma 'tuwa:g' na nufin kwartanci. Ma'ana, namiji mai yin kwartanci = buga:botuwa:g. Idan kuwa kwartuwa ake magana, sai saiwar ta sami xafin `bo'o:` - mai nufin mace, sai `-bo-` da ke nuni da yin abu, `tuwa:g` kuma kwartanci kenan mace mai yin kwartanci, sai a ce bo'o:botuwa:g wanda ke nufin kwartuwa. Ga wasu qarin misalai :*

buga:botuwa:g 'kwarto:' bo'o:botuwa:g 'kwartuwa'

buga:boyeb 'xangida' bo'o:boyeb ''yargida'

buga:bo'ege:t 'mai abu' bo'o:botu'ege:t 'mai abu'(mace)

Mafi yawan kalmomin suna ko sifa a harshen Kamuku ba su cika samun bambanci na jinsi ba.

4.2Kumburin Samar Da Suna Na Asali :

Wannan ya qushi yadda akan sami sunan mai harshe sakamakon kumburin sunan na harshe. Misali;

Hausa – Bàhaushè,

Nufe – Bànufè

Gwa:ri – Bàgwa:ri:

Kanò: – Bàkanò: da sauransu.

A harshen Kamuku kuwa,

Kùya: - Hausa bukùya: - Bàhaushè:

Tunufawa - nufe bunufawa - bànufè

Gwa:r - gwari bugwa:r - Bàgwa:ri:, da sauransu.

4.3 Jam'antawa A Harshen Hausa

Fagge (2012 shf 30) ya bayyana tsarin jam'antawa da: tsarin tasarifi ne na qara xafi a saiwar kalma don iyakance tasirinta a nahawu, kuma ya kasance xafin bai haifar da sabuwar kalma a rukunin nahawudaban ba, sai dai nuni da rukunin nahawu kamar jinsi da adadi. Haka kuma, Abdulkadeer (2006) ya bayyana cewa, kalmar jam'i, kalma ce wadda aka aro daga Larabci da ke nuna abu fiye da xaya.

Jam'antawa a tasarifin Hausa wani muhimmin vangare ne a fannin nazarin kimiyyar harshe, ganin yadda masana suka yi ta kai-komo wajen ganin sun samar da wani tsari na musamman gare shi. Sai dai hakan bai samu ba, saboda rashin samar da takamaimiyar qa'ida ta bai xaya. Misali, manazarta harshen Hausa na farko-farko kamar Parsons (1960) ya fitar da azuzuwa goma na jam'anta kalmomin suna na Hausa. Haka kuma Mukoshy (1978) ya kalli jam'antawa, inda ya karkasa ta zuwa azuzuwa takwas, waxanda ya kira ginshiqan tsare-tsaren da kuma na gama-gari ainun da na gama-gari da kuma na qirqire. Kraft da Kirkgreene (1980) ma sun fitar da azuzuwa goma sai dai sun karkasa zuwa manyan kashe-kashe huxu... Zaria (1999) kuwa fitar da azuzuwa tara ya yi, ta

hanyar sa makoyi haddar tsarin jam'antawa na kowane aji kamr dai yadda Abdulkadeer (2006) ya bayyana a aikinsa.

Shi kuwa Abubakar (2001) ya samar da azuzuwan jam'antawa har guda ashirin da biyu ta hanyar samar da qwayoyin ma'ana na jam'antawa a kalmomin Hausa ta la'akari da tsari da karin sauti ko wasali na bai-xaya ga kowane aji, da sauransu.

Fagge (2004) ma ya fitar da wasu tsare-tsare na jam'antawa tare da bayar da misalai na kalmomi qarqashin kowane tsari da ya kawo don qara fayyacewa, ya kuma nuna wuraren da ake amfani da xafa-ciki da xafa-qeya don samar da kumburi wajen jam'antawa. Har ma da tsarin jam'antawa na qage ko qirqire wanda ya kira da '*exaggerative plural form'.*

Wannan aiki da ake gudanarwa yanzu, ya bibiyi kumburi, da fitar da qwayoyin ma'ana da kan haifar da kumburi a harshen Hausa da na Kamuku.

A Hausa, ana amfani da qwayar ma'ana ta *–una* wadda ake xafa wa saiwar kalma a qarshe (xafa-qeya) ta kumbura ta samar da jam'i. Misali,

Xafa-qeya -una

1 rì:ga: – ri:gunà:

2 kè:ke – ke:kunà:

3 bàrgo: – bargunà:

4 kànti: – kantunà:

Xafa-qeya -*uka*:

1 launì: – launukà:

2 la:yì – laayukà:

3 qauyè: – qauyukà:

4 ra:mì: – ra:mukà:

5 rà:fi: – ra:fukà:

Xafa-qeya -*kuu :*

1 ra:na: – rà:nàku:

2 za:na: – zà:nàku:, da suaransu.

Akwai xafa-qeya mai tsarin -*oob$_2$ii*, inda ake samun dogon wasali na /oo/ sai baqi na qarshe a jerin baqaqen da ke cikin kalmab$_2$na nuni gabaqi na biyu, wato ga kalmomi masu gavovi bibiu a kalmar da abin ya shafa sannan sai dogon wasali na /-ii/ a qarshe. Misali,

1 igiyà: - igiyo:yi:

2 qo:fà: – qo:fo:fi:

3 kamfàni: – kamfano:ni:

4 mo:tà: - mo:to:ci:

5 le:dà: – le:do:ji:

6 re:zà: – re:zo:ji: da sauransu.

Xafa-qeya –à*ayée*:

1 gaula: – gaulà:ye:

2 wa:wa: – wa:wàaye:

3 gwàni: – gwànà:ye:

4 ve:ra: – ve:rà:ye:

5 mu:gù: – mu:gà:ye:

6 be:be: - be:bà:ye:

7 do:lo: - do:là:ye:

Xafa-qeya –*aab*$_2$*ee*, (b_2 = baqi na biyu na kalma) kamar,

1 baqi: – baqà:qe:

2 gado – gadà:je:

3 quda: – quda:je:

4 gida: – gidà:je:

5 ruga: - rugà:ge: da sauransu.

Xafa-qeya –*aab$_3$w*(inda ake samun dogon wasali /aa/ sai baqi na uku na kalma, sannan dogon wasalin /ee/ ko /aa/), kamar:

1 kasko: - kasà:ke:

2 qwalba: – kwalà:be:

3 birni: – birà:ne:

4 jirgi: – jirà:ge:

5 damtsè: - damà:tsa:, da sauransu.

Xafa-qeya –*ii :*

1 qwà:ro: – qwà:ri:

2 hànka:kà: – hànkà:ki:

3 bà:qo: – bà:qi:

4 zà:bo: – zà:bi:

5 fà:ra: - fà:ri:, da sauransu.

Xafa-qeya –*aa :*

1 malà:là:ci: – malà:là:ta:

2 mahàlbi: – mahàlba:

3 manò:mi: – manò:ma:

4 magùlmàci:, magùlmàta:

5 mahàukàci: – mahàukàta: , da sauransu.

Xafa-qeya–*uu* :

1 qò:nanne: - qò:nànnu:

2 sò:yayye: - sò:yàyyu:

3 wànkakke: – wànkàkku:

4 mì:qaqqe: - mì:qàqqu:

5 xàmmara: – xàmmàru:

6 lànqwàsasshe: – lànqwàsàssu: da sauransu.

Xafa-qeya –*ai :*

1 dàli:lì: – dàlì:lai

2 jà:ri:ri: – jà:rì:rai

3 macì:ji: – màcì:zai

4 wàli:yi:- wàlì:yai

5 àmi:ni: - àmì:nai, da sauransu.

Xafa-qeya –*ub$_2$uwaa:*

1 Gàri: - garu:ruwà:

2 bù.ki: – buku:kuwà:

3 qirà:re: - qira:ruwà:

4 qàshi: – qasu:suwà:

5 xàri: - xaru:ruwà:

Xafa-qeya *–aawaa*. Misali,

1 Bàhaushè: – Hàusaà:wa:

2 Bàtu:rè: - Tù:rà:waa:

3 Bàqauyè: – Qàuyà:wa:

4 Bàla:rabè: - La:raba:wa:

5 Bànu:fè: – Nufa:wa:

Xafa-qeya *–$b_2$aa. A* wannan tsari akan samu ninkin baqi na biyu na kalma, sannan sai wasalin aa. Kamar;

1 Si:sì: - sìssa:

2 qa:tò: - qaàtta:

3 shu:xì: - shùxxa:

4 zo:bè: – zòbba:

5 ko:rè: – kòrra:

Xaf-qeya *–$b_2$ai. Kamar a,*

1 kwabò: – kwàbbai

2 qasà - qàssai:

3 dubu: - dùbbai

4 samà - sàmmai

5 tsirò: – tsìrrai.

6 dami - dàmmai

Xafa -qeya *–annii* . Kamar

1 kà:ka - kà:kànni:

2 dò:do: – dò:dànni:

3 watà: – wàtànni:

4 fùre: – fùrànni:

5 wà:sa: - wà:sannii

6 kà:suwa: - kàsu wanni: da sauransu.

Xafa-qeya *–a…ai.* Misali,

1 marmara: - màrà:màrai

2 fuffukè: - fùkà:fùkai

3 tsuttsugè: - tsùgà:tsùgai,

4 duddugè – dùgà:dùgai

5 kwarkwaroo – kwàrà:kwàrai

Xafa-qeya *–$b_4$aa.* Misali,

1 mùmmuuna: - mu:nà:na:

2 Kyàkkya:wa: - kya:wà:wa:

3 fàffaaxa: - fa:xà:xa:

4 kàkkaura: - kaurà:ra:

5 zàzzaafa – za:fà:fa:

Zarruq (1999 shf 10-12) ya nuna cewa akwai wuraren da ake amfani da qwayoyin ma'ana –*xan*- da -*'yan*- da –an- a matsayin xafa-ciki don motsa kalma daga tilo zuwa jam'i a wasu kalmomin Hausa. Misali:

1 wannan - waxannan (wa'yannan ko wa'annan)

2 wancan - waxancan (wa'yancan ko wa'ancan)

3 waccan - waxancan (wa'yancan ko wa'ancan)

4 wanda - waxanda (wa'yanda ko wa'anda)

5 wanne ? - waxanne ? (wa'yanne ? wa'anne?)

Xan da 'yan da kuma an, waxanda aka ja wa layi qarqashi cikin misalan da suka gabata, su ne suke nuni da qwayoyin ma'ana da aka xafa cikin saiwoyin kalmomin (tsakiyarsu), kuma suka kumbura don samar da jam'i.

Haka kuma akan yi amfani da –aa- a matsayin xafa-ciki don samar da jam'i. kamar wajen jam'in :

1 gurgù: - gurà:gu:

2 falke: – falà:ke:

3 murhù – mura:hu:

4 sarki: – sàrà:ki:

5 barde: - barà:de:

6 marke: - marà:ke:, da sauransu.

Baalou (1997 shf 48-57) ya fitar da yadda jam'in wasu kalmomin harxaxxun sunaye suke kasancewa wato inda kumburin yakan shafi kalmomin da ke vangaren hagu ne kaxai. Misali:

1 hù:lar-kwa:nò: hu:lunàn-kwanò: ba **hu:lunàn-kwa:noni ba.*

2 rì:gar-ruwa ri:gunan-ruwa ba **ri:gunan- ruwà:ye; ba.*

3 gidân-sauro: gidà:jen-sauro ba **gidà:jen-saurà:ye: ba.*

4 qudân-zumà - qudà:jen-zumà ba **quad:jen- zumomi ba*, ds.

Haka kuma Zarruq (1999 shf 4) ya qara bayyana cewa , an lura da cewa , qusoshin motsa kalma daga tilo zuwa jam'i, irin su nau'in xafi ko na ninki da musayar wasali a gaban harafin jam'i ko kuma a tsakiya ko kuma bayansa, duka abu xaya ne ake samu a qarqashin kowane aji. Misali:

1 bùka:tà: – bùkà:ce:-bùkàce:

2 gudù: - gùje-gùje:

3 halbì: - hàlbe-hàlbe:

4 àkà:wu – àkà:wu-àkà:wu

5 kàlôb - kùlôb-kùlôb

6 xagwas - xagwas-xagwas

7 mì:tsi:tsì - mitsi-mitsi, da sauransu.

Akwai kuma kalmomin da suke da nau'o'in kalmomin jam'i fiye da xaya a Hausa. Misali :

1 àbù – abu:buwà:, abubbà:, abà:ba:, abà:bai, abaibaxai

2 kada: - kaddunà, kada:dunà, kada:duwa, kaddai, kàdànni:, kadannu, kadùnni:, kado:di:, kado:ji:

4 cìniki: - cìnikai, cìnikkai, cìnukkà:, cìniko:ki:, cìnìke-cìnìke:.

5 àlmakàshi: - àlmàkàsai,àlmàkassai,almakasà:, almakassà, da sauransu.

duk waxannan, misalai ne na jam'antawa a Hausa.

4.4Jam'antawa A Harshen Kamuku

Mashegu (2008 shf 5-11) ya kawo tsarin qirga a harshen Kamuku sannan a qarshe ya kawo xafe-xafen da ke haifar da jam`antawa a harshen na Kamuku. Mashegu (2008 shf 11-15) ya yi qoqarin bayyana yadda tsarin jam`antawa yake a harshen Kamuku ta hanyar nuna qwayoyin ma'anar da

akan xafa, kuma ana yin xafin ne a farkon saiwar kalma, wato xafa-goshi. Qwayoyin ma`anar da ake amfani da su sun haxa da: *she-* da *sha-* da *mo-* da kuma *mu-* Misali : *àma:ci – shèma:ci* (tso:huwa: - tsò:fàffi:), *ana:ta – shena:ta* (gizògizò - gizògizò), *a:wa – sha:wa* (kàre: – karnukà:), *amàh – sha:mah* (birìbirai), *èno:no - mòno:no* (tsuntsu:-tsuntsàye:), *eyra-mò'eyra* (kibiyà – kibiyo:yi:), *e:shè - mò'e:shè* (idò: - ida:nuwà:), *ìma:ma – mùma:ma* (tukunya: - tukwà:ne:), *ìtu:tu – mùtu:tu* (jàka: - jakkunà:).

Akwai kuma inda ake jam`in kalma ta hanyar xafa-goshin wasalin *a:-*. Misali, *u:hi:* + *a:-* **a:u:hi:* (wasali da wasali ba su haxuwa, don haka sai *u:* ya kauce wa xafa-goshi na *aa-*) a sami *aahi:*.

KAMUKUMA'ANA

Ù:hi: – à:hi: (kâi – ka:wunà:)

Ono:no - a:no:no (àku - àku).

Binciken da aka gudanar sakamakon zantawa da aka yi da Kamukawa, ya sa an fitar da qwayoyin ma'ana masu jam'anta kalma a harshen Kamuku ta hanyar kumbura kamar haka: shi- , she-, sha-, mu-, mo, aga-, a-, da ee-. Kamar waxansu misalai :

Xafa-goshi *shi-*

	TILO	**JAM'I**
1	àhu:g - wuri:	shìhu:g – wura:re:
2	*à:bes* - tsintsiya:	*shibes* - 'tsintsiyò:yi'
3	*ànà'ubà:n* -qo:fà:	*shìna'ubà:n* – qo:fo:fi:
4	*àhinginu* - muciya:	*shìhinginu* - muciyò:yi:
5	*ogig* - lu:dàyi:	*shigiig* - lu:dayà:
6	*uban - qyaure:*	*shi'uban 'qyamà:re:'*
7	*aazangata - ra:riya:*	*shizangata - ra:riyo:yi:*
8	*anaata gizo-gizo*	*shi'anaata - gizo-gizo*
9	*rwaag - gulbi:*	*shirwaag - gulà:be:*
10	*amaac - tso:huwa:*	*shi'amaac - tso:fàffi:*

Xafa-goshi *she-*

	TILO	**JAM'I**
1	*a:p*[1] - rì:ga:	*shè:po:* - ri:gunà:
2	*agangunà* - qàdangarè:	*shègangunà* - qàdàngàru:
3	*a:sumb* - cìnna:ka:	*shèsumb* - cìnnà:ku:[i]

4	*anwa:* - sauro:	*shênwa:* - ‘sauro:’
5	à’ob - fa:tà	shè’ob – fa:to:ci:
6	*abob* - re:shè:	*shèbob* - râssa:
7	*aaho* – macì:ji:	*sheeho* - màcì:zai

Xafa-goshi *sha-*

	TILO	**JAM’I**
1	*a:bor* - màtankaxi:	*sha:bor* - matankuxà:
2	*a:b* - ba:ya:	*sha:b* - ba:ya:
3	*a:maà* - biri	*sha:mà* – ‘birai
4	*a:ròm* - kà:za:	*sha:ròm* - kà:ji

Xafa-goshi *mu-*

	TILO	**JAM’I**
1	*i:’ob* - fartanya	*mu’ob* - fartànyu:
2	*i:’ab* gà:tari:	*mu’ab* - ga:turà:
3	*saka:r* - kwàndo:	*musaka:r* - ‘kwandunà:
4	*i:gurc* - guntu:	*mugurc* - guntàye:
5	*kesh* - ku:ra:	*mukesh* - ku:rà:ye:
6	a*sha:b* - magirb	*musha:b* - magirbai
7	*ce:p* - birni	*muce:p* - birà:ne:

8	*i:sh* - ido	*mu'i:sh* - ida:nuwa

Xafa-goshi *mo-*

	TILO	**JAM'I**
1	*e:*[1]*nò:n* - tsuntsu:	*mono:nò*[1] - tsuntsà:ye: (qanana)
2	*eyr* - kibiyà:	*mo'eyr*[2] - kibiyo:yi
3	*e:rà:* - su:rì	*mo'e:rà:*[3] – su:rì
4	*e:rà:b* - gyàxa:	*mo'e:rà:b*[4] – gyàxa:

Xafa-gishi a-**:**

	TILO	**JAM'I**
1	*buzumb* - vàra:wò:	*a:zumb*[5] - vàrà:yi:
2	*ye:gwa* - zà:bo:	*a:yè:gwa* – zàbbi:
3	*buga:* - mutum	*a:ga:*[6] – mutà:ne:
4	*bo'*[7] - xa:	*a:'* [8] - 'ya:'ya:
5	*uye* – kabàri:	*a'uye* - kaburburà:

[1] e:no: + {mo-} (xafin jam'i)-moe:no:n (qirar voye)-mono:n (shafe wasali)-mono:n (qirar sarari/lafazi).

[2,3] da [4] tsarin nasu babu share wasali.

[5] buzumb + {a-} (xafin jam'i)-abuzumb (qirar voye), azumb (share gava)-azumb (qirar sarari/lafazi).

[6] shima tsari kamar na 5 ne

[7] Akwai baqin hamza a qarshen gavar kalmar, kamar irin ta kalmar a''auna ta Hausa. Haka lamarin yake ga[8].

6	*ruma:g* - ra:go:	*a:rumag* - ra:gunà:
7	*o:bomb* - ganye:	*a:bomb* - ganyà:ye:
8	*o:g* - zàkàrà:	*a:'o:g* - zàkàru:

Xafa-goshi agaa- :

	TILO	**JAM'I**
1	*bùga:bottom* - manò:mi:	*aga:tom*[9] – manòma:
2	*bùga:bopyap* - maqè:ri:	*aga:pyap*[10] – maqè:ra:
3	*bùga:buzò:g* - mawà:qi:	*aga:zò:g*[11] – mawà:qa:
4	*bùga:busu* - masùnci:	*aga:su*[12] – masùnta:
5	*bùga:bumagyar* - mahalbi:	*aga:magyar*[13] – 'mahalba:'
6	*buga:bo'okic* - maqàryaci	*aga:'okic*[14]- maqàryàta:

Xafa-goshi ee-

	TILO	**JAM'I**
1	*onà* - wannàn	*e:n*[15] – waxannàn
2	*bena* – sâ:	*e:na*[16] - sha:nu:[2]

[9]buga:buzo:g + {a} (xafin jam'i) abuga:buzo:g (Qirar voye), aga:buzo:g (shafe gava ta farko), aga:zo:g (shafe gava ta biyu), aga:zo:g (Qirar sarari/ lafazi). Haka abin yake ga lambobin [10, 11, 12,13 da 14]

[15] ona + {e} (xafin jam'i), e:ona (qirar voye), e:na (shafe wasali), e:n (shafe wani wasalin),e:n (qirar sarari/lafazi).

[16] bena + {e} (xafin jam'i), ebena (qirar voye), e:na (shafe gava), e:na (qirar sarari/lafazi).

Waxannan su ne misalai na jam’antawa a harshen Kamuku.

Dangane da binciken da aka gudanar, an gano wasu qarin qwayoyin ma’ana / aga:-/ da /ee-/waxanda kan haifar da jam’antawa a harshen Kamuku. Wato qari bisa ga waxanda aka kawo yayin bitar ayyukan da suka gabata.

Daga jawaban da suka gabata an nuna yadda harshen Hausa da na Kamuku suke amfani da xafi wajen mayar da kalmar tilo zuwa jam’i. Hakan dai yana nuni da cewa kalmomin sun fito ne daga tushe xaya, kuma sauyin zuwa jam’i yana faruwa ne ta hanyar kumbura. A Kamuku shi- da aga- da mu- da she- da sauransu xafa-goshi ne da ake qara wa saiwar kalma, a Hausa kuwa, akwai xafa-qeya -una, -obii, -aayee, -aa da sauransu, sai kuma xafa-ciki kamar -xan- da –a- da ake qara wa saiwar kalma wajen samar da jam’i.

Haka kuma harsunan Hausa da na Kamuku sun yi tarayya wajen amfani da qwayar ma’ana ta {a} don jam’antawa, kamar a misalan yaro-yara, mahalbi-mahalba murhu- murahu, falke-falake,da sauransu a Hausa, haka kuma yegwa-ayegwa, buga, aga, da sauransu a harshen Kamuku . Sai dai cewa a Hausa xafin na {a} na zuwa ne a matsayin xafa-qeya, amma a

Kamuku xafin na jisintawa kan zo ne a matsayin xafa-goshi, kamar yadda muka gani a misalan da suka gabata.

Duk da cewa harsunan biyu suna amfani da xafi ne, wajen jam'antawa, to amma harshen Kamuku yana amfani ne da xafa-goshi kawai, savanin Hausa mai amfani da xafa-qeya da xafa-ciki wajen jam'antawa.

A harshen Hausa, akwai wasu kalmomi waxanda ba su da wani bambanci na adadi. Ma'ana, da tilo da jam'i duk xaya ne, kamar tùru:ruwa:, zumà:, rina: , qya:ya: , shàzuma:mìi da sauransu. Harshen Kamuku ma yana da irin wannan tsari misali ; e:sùn 'zuma' , gàmuyyai – 'tùru:ruwa:', rend-'rina' da dai sauransu.

Haka kuma, akwai wasu kalmomin da kalmar jam'i da ta tilo ba su da wata nasaba dangane da saiwarsu, kamar su do:kì: - go:xiya:, sauràyi – bùdurwa:, xa: - 'ya:, babba-manya, àkuyà: – bùnsuru:, rà:goo – tunkìya:, rà:qumi: - tà:guwà: da sauransu. Dangane da binciken da aka gudanar harshen Kamuku ma yana da irin wannan tsari na lamuni ko jinga, misali; rùma:g – bitem (rà:go: - tinkiya:), beny – rùigu: (akuya – bunsuru).

A Hausa akwai wani tsarin kumburin na kalmomin aikatau, inda kalma takan kumbura ta samar da ma'anoni daban-daban. Misali, buga-

buge- bugi-bugo-bugu da bugar. Ko harba-harbe-harbi-harboda harbu, duk irin waxannan kalmomi ne na aikatau da suke samuwa sakamakon xafin qwayar ma’ana, wanda kuma kowacce take qunshe da wata qarin ma’ana. Dangane da binciken da aka gudanar harshen Kamuku ba shi da wannan tsari.

4.5Bayanau Na Yanayi:

Wannan ya qunshi kalmomi ne masu nuna yadda abu ya kasance, misali;

tsaye- tsattsaye zaune zazzaune

jingine- jijjingine kwance-kwakkwance da sauransu.Ga misali a Hausa da Kamuku ;

ìsa:ge - tsàye isa:gàge - tsàttsàye

nakya - zàune nakya:ge - zàzzàune

shinjigai - jìngìne shinjiga:ge - jìjjìngìne.

uran –xaure urangani- xaxxaure

yabci – kwance yabtagi kwakkwance

Abinciken da aka gudanar baki xaya, a wajen nuna bayanau na yanayi ne kaxai Kamuku ke amfani da xafa-qeya wajen kumbura kalma.

4.6Kammalawa

A wannan babi, an nuna yadda ake samun kumburi ta fuskoki daban-daban wajen qirar kalmmomi, tare da qwayoyin ma'ana da ake amfani da su, da misalan yadda akan sarrafa su a harshen Hausa da Kamuku, kama daga yanayin jam'antawa , zuwa jinsintarwa na harsunan biyu inda aka bayar da misalai tare da nuna wuraren da xafin kan shafi saiwar kalmomi a harsunan biyu, don qara fayyace batun da ake bincike.

BABI NA BIYAR

TAQAITAWA, KAMMALAWA DA SHAWARWARI

5.0Gabatarwa

Wannan babi zai kalli abubuwan da aikin ya qunsa a taqaice. Hakan zai ba da damar amsa tambayoyin bincikenmu. Tambayoyin kuwa, su ne : Ko harsunan biyu suna amfani da qwayoyin ma'ana iri xaya ne wajen kumbura kalma, ko kuwa akwai yiwuwar samun kamanceceniya da bambance-bambance na ire-iren xafin da harsunan ke amfani da su ? Ko an tabbatar da hasashen da akayi tun farkon wannan aiki, na yiwuwar samun xafin da harsunan biyu suka yi tarayyar amfani da shi da kuma wanda kowane harshe ya kevanta da shi? A qarshe kuma, aikin zai bayar da shawarwari.

5.I Taqaitawa

Sakamakon binciken da aka gudanar ya nuna yadda harshen Hausa da na Kamuku suka yi tarayya wajen yin amfani da xafin qwayar ma'ana don kumbura kalama,ta hanyar ko daiamfani da xafa-goshi ko xafa-ciki ko kuma xafa-qeya, wanda akan manna wa saiwar kalmadon kumbura ta. Haka

kuma, a vangaren kumburi wajen jam'anta kalma, Hausa da Kamuku sun yi tarayyar amfani da qwayar ma'ana ta {a}da ake xafa wa saiwar kalma wajen jam'antawa, duk kuwa da cewa a harshen Hausa qwayar ma'anar ta {a} xin kan zo ne a matsayin xafa-ciki da xafa-qeya, alhali kuwa a harshen Kamuku, takan zo ne a matsayin xafa-goshi kaxai don jam'antawa.Wannan ke nuni da cewa Hausa da Kamuku sun yi tarayyar amfani da tsarinliqa qwayar ma'ana a matsayin xafa-qeya wajen mayar da kalma tilo ta koma jam'i. Har wa yau kuma harshen Hausa, baya ga amfani da xafin na {a} don jam'antawa, Hausa na yin amfani da xafin na {a} a matsyin xafa-qeya don jinsintarwa.

Ta fusakar kumbura kalma don samar da suna na asali a harsunan biyu kuwa, harsunan sun yi tarayyar yin amfani da xafa-goshi (ba/bu) duk kuwa dacewa Hausa na amfani da xafa-goshi na 'ba' harshen Kamuku kuma na amfani da 'bu', (watobambancin wasali. Yayin da harshen Hausa ke amfani da 'ba' mai wasalin a, harshen Kamuku na amafani da 'bu' ne mai wasalin 'u') kamar misalan 'gwari- bagwari' a Hausa da kuma 'gwaar-bugwaar' a Kamuku. Kenan harsunan biyu sun tarayyar amfani da xafa-goshi 'ba' da 'bu' masu kama da juna don kumbura kalma.

Idan kuma aka koma vangaren bambance-bambancen da ke tsakanin harshen Hausa da na Kamuku suke amfani da xafi wajen kumbura kalma, an ga yadda Hausa take amfani da xafi iri uku, wato xafa-goshi da xafa-ciki da kuma xafa-qeya wajen kumbura saiwar kalma. Shi kuwa harshen Kamuku xafa-goshi da xafa qeya yake amfani da su wajen cin ma wannan manufa. Domin kuwa, a binciken da aka gudanar, ba a sami wuri ko da guda xaya, inda harhen Kamuku ya yi amfani da xafa-ciki wajen kumbura saiwar kalma ba. Kenan dangane da sakamakon binciken, za a iya cewa amfani da xafa-ciki wajen kumbura saiwar kalma ya kevanta ne da harshen Hausa kaxai.

Waxansu abubuwan kuma da harshen Hausa ya kevanta da su, sun haxa da: Tsarin samun canjin azuzuwa na aikatau, kamar harba – harbe – harbi – harbo – harbu, da sauransu,wanda babu wannan tsari a harshen Kamuku. Hakan kenan yake nuni da cewa Hausa da Kamuku sun yi tarayyar amfani da xafa-goshi da kuma xafa qeya domin kumbura kalma.

5.2 Kammalawa

A babi na farko, an kawo tarihin Hausawa da Kamukawa a taqaice, da alaqar da ke tsakaninsu. An kuma nuna dalili da kuma manufar bincike tare da muhimmancinsa, sannan aka kawo farfajiyar bincike gami da tambayoyi da hasashen bincike.

Babi na biyu ya bibiyi ayyukan magabata ne, inda aka duba fahimtarsu, kama daga bugaggun litattafai zuwa kundayen digiri, da mujallu da muqalu da kuma takardun qara wa juna sani, musamman ta fuskar abin da ya shafi kumburi, domin kwatantawa tsakanin harshen Hausa da na Kamuku. Ma'ana, dukkansu ayyuka ne masu dangantaka ta kusa da ta nesa da wannan aiki da ake gudanarwa.

A babi na uku, an bayyana hanyoyin da aka bi wajen gudadnar da binciken , kama daga ziyartar xakunan karatu da garuruwan Kamuku da yadda aka tattara bayanai da sarrafa su, har zuwa inda aka bayyana irin ra'in da aka xora aikin binciken.

Bayanan da aka tattara gami da misalai a babi na huxu, sun bayar da damar kwatanta yadda lamarin kumburin saiwar kalma yake a harshen Hausa da na Kamuku.

A babi na biyar kuma an fitar da wuraren da harsunan biyu suka yi tarayya da kuma inda suka bambanta. Hakan kuma ya sa aka kai ga samun amsoshin tambayoyin bincike tare da tabbatar da hasashen da aka yi tun farkon aikin.

5.3 Shawarwari

Ganin cewa nazarin kimiyyar harshe ya qunshi manyan vangarori irin su: Tsarin sauti da Tasarifi da Ginin junla da kuma Ilimin ma'ana, wannan aikin ya kalli wani sashe ne na tasarifi, kamata ya yi a faxaxa bincike, musamman a kan harshen Kamuku don a yawaita nazari, a adana.

Hukumomi da qungiyoyi masu zaman kansu da sauran xaliban ilimi su haxa qarfi wajen xaukar nauyin gudanar da bincike kan harsunan qasa don a taskace su a kuma kare su daga barazanar da suke fuskanta ta vacewa daga doron qasa.

Haka kuma, an yi kira da babban murya ga hukuma da ta sa a rinqa koyar da karatu da harshen uwa a aji uku na farko na firamare, don ta haka

za a taimaka wajen samar da hanyar karatu da rubutu na qananan harsunan qasa a duk wuraren da ake amfani da su.

Haka kuma ya kyautu jami'o'i su qara qwazo wajen ganin ana mayar da hankali kan nazartar harsunan qasa yadda za a bunqasa su sosai.

MANAZARTA

Abubakar, A. (2001). An Introductory Hausa Morphology. Department of Languages and Linguistics, University of Maiduguri. Nigeria.

Abubakre, S.O. (2008). Affixation In Hausa and Eggon: A comparative analysis Journal of Linguistics, Litereature and Culture. Department of Linguistics and Nigerian languages, University of Ilorin, Ilorin Nigeria.

Abdulkadeer,M.(2006). Jam'antawa: Nazari a kan Kwatanta Jam'in Hausa da na Turanci, PGDHS, Sashin Koyar da Harsunan Nijeriya Jami'ar Bayero, Kano.

Adamu, M.T. (1997). Asalin Hausawa Da Harshensu. Kano Xan Sarkin Kura Publishers.

Alhassan, B.S.Y.(2010). InfixationinHausa.Unpublished Paper.Zaria:Ahmadu Bello University.

Aminu, A.Y.(2011).Nazari A Kan Jam'in Kalmomin Aro Sabbi Daga Harshen Turanci da na Larabci Zuwa Hausa. Kundin Digiri na Farko , Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero Kano.

Aujara,A.A.(2012).Kalmomin Larabci A Hausa da Sauye-sauyen Ma'anarsu. Kundin Digiri na Uku, Jami'ar Bayero, Kano.

Baalou, K. (1997). A Lexical Analysis of Hausa Morphological Strata Ordering. MA Thesis Department of Nigerian Languages, Bayero University, Kano.

Baba, N. (2006), Kwantanta Tasarin Hausa Dawa Larabci Kundin Digiri Na biyu (MA) Sashin Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Bargery, G.P. (1993). A Hausa-English Dictionary And English Hausa Vocabulary. Second Edition, Ahmadu Bello University Press Ltd, Ahmed Talib Building, Zaria-Nigeria.

Bobi, B.A. (2008).Asalin garin Bobi da Bukin Uhyana. unpblished Government secondary Scool Bobi, Niger State.

Busa, M.A. (2012).Comparative Study Between Hausa and Gbagyi Sound System. Department of Nigerian and African Languages and culture, Ahmadu Bello University, Zaria.

Chomsky, N. (1965). Aspect of Theory of Syntax, Cambridge MA MIT Press.

CNHN (2006) Qamusun Hausa na Jammi`ar Bayero, Kano.

El-Hassan, S. (1993). The Morphology, of Loan words in Linguistics, University of Maiduguri.

Fagge, U.U. (1980). Aspect of Hausa Morphology. Kundin digiri na biyu,Jami'ar Bayero, Kano.

Fagge, U.U. (2004).Introduction to Hausa Morphology. Gidan Dabino Publishers, Kano.

Fagge, U.U. (2012). Hausa Language and Linguistics. Ahmadu Bello University Press, Zaria, Kaduna State, Nigeria.

Fagge, U.U. (2012) Qirar Kalma a Hausa.Ahmadu Bello University Press, Zaria, Kaduna State. Nigeria.

Galadanci, M.K.M. (1976) An Introduction to Hausa Grammar, Longman Ibadan.

Gambo,M. (2009)Xafi A Ginin Kalma: Kwatance Tsakanin Harshen Hausa da na Ingilishi. Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Greenberg, J.H. (1963). The Languages Of Africa, Bloomington: Indiana University.

Greenberg, J.H. (1990) Language Selected Reading. Standford University Press.

Gital, G.M. (1983). The Phenomenon of Transformational Syntax, BA Project, Deparment of Nigerian Languages, Kano: Bayero University.

Halima, A.S. (2011). Resources Of Hausa Inflectional Formations. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano. B.A Dissertation , Faculty of Arts and Islamic Studies, Bayero University, Kano.

Idris, J. (2014)Nazarin Wasu Kalmomin Hausa Ta Fuskar Qira Da Kain Sauti Da Kuma Ma'ana, Kundin Digiri na Farko, Jami'ar Bayero, Kano.

Imam, H.F. (2010). Kamanci Da bambanci Tsakanin Hausa Da Larabci Ta Fuskar Qirar Kalma. Kundin Digiri Na Biyu, Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Jinju, M.H. (1981). Rayayyen Nahawun Hausa, Northern Nigerian Publishing Company, Zaria.

Jinju, M.H. (1985). Asalin Hausawa da Harshensu. Takarda Da Aka Gabatar, a Taron Qasa da Qasa na uku a kan Harshe da Adabi , Cibiyar Nazarin Harasunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Katamba, F. (1993) Morphology Macmilan Press Limited.

Kure. A. (2014). Assesment of Traditional Method of Conflict Resolution In Kagara Emirate of Rafi Local Government Area of Niger StateB.A Disserttion, School of Arts and Social Sciences, National Open University, Minna.

Kwakwaci, K.H.(2010). Asalin Hausawa , Harsashi Printing Press, Kano, Nigeria.

Ladan, Y. (1981). Tasarifin Hausa. Takarda da aka Gabatar a Taron Qasa na Biyu a kan Harshe da Adabi da Al'adu na Hausa. Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Lamidi,M.T. (2008). Aspect of Chomskyan Grammar . Ibadan University Press, plc.

Lyons, J. (1968). An Introduction to Descriptive Linguistics. Cambridge, Cambrige University Press.

Maikuxi, D. (2008) Conperative Analysis Of Hausa And Yoruba Adjectival Phrase, B.A Desertation, Department of Nigerian Languages, Bayero University Kano.

Maryam, I.A. (2007). Nazarin Kamanni Da Bambanci Tsakanin Harshen Hausa Da Ingilishi Ta Fuskar Jinsi. Kundin Digiri Na Farko, Jami'ar Bayero, Kano.

Mashegu, A.B. (2008). The Category Of Number In Kumuku. An MA Seminar paper Presented At The Department Of Linguistics And Nigerian Languages, Universty Of Ilorin, Nigeria.

Meek, C.K. (1958). The Northern Tribes Of Nigeria.Oxford University Press.

Mohanan, K. P. (1982). Lexical Phonology. *MIT. Dissertation. IUTC.*

Mohammed, D.(1990). Huasa metalanguag. (Qamus na kevavvun kalmomi) vol 2, University Press Ibadan.

Mukoshy, I.M. (1978). Hausa Plurals Proces. Paper presented at the First International Conference on Hausa Language, Literature and Culture, Centre for the study of Nigerian Languages, Bayero University, Kano.

Mukoshy, I.A. (1984). The Sound and Morphemes of Fulfulde. An Examination of Fulfulde Phonology, Deparment of Nigerian and African Languages and Cultures, Ahmadu Bello University, Zaria.

Musa, T.M. (2014). Kwatancin Ginin Kalmar Hausa Da Na Badanci. Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Nakuta, A.A.I. (1999). Tarihin Qasar Birnin-Gwari. Body Production, Gwari Road, Kaduna.

Newman, P. (1967) Feminine Plurals in Hausa; A Case of Overcorrection.

Newman,P.(2000).The Hausa Language:An Encyclopedic ReferenceGrammar.New Haven:Yale University Press.

Pandogari, S.I. (1990) Administration of Justice in Kamuku Land : A case Analysis of the Role of Traditional Rullers (1900-1988). B.A Dessertation, Faculty of Social Sciences and Administration, Usman Xanfodio University, Sokoto.

Rufa'i,A.(1986). Qoqarin Shawo Kan Jam'i a Hausa.Presented at Departmental Seminar Nigerian Languages.Kano:Bayero University.

Sani, M.A.Z. (1999). Tsarin Sauti da Nahawun Hausa. Ibadan University Press Plc.

Sani, M.A.Z. (2002).Alfiyyar Mu`azu Sani 1. Tsarin Sauti da Tasarifin Hausa a Waqe. Benchmark Publishers Limited, Kano, Nijeriya.

Sani, M.A.Z. (2011). Gamayyar Tasarifi Da Tsarin Sautin Hausa. Zaria, Ahmadu Bello University Press Limited, Kaduna State Nigeria.

Sani, M.A.Z. (2013). Maraka Yanki A Tsarin Sautin Hausa Zaria, Ahmadu Bello University Press Limited, Kaduna State Nigeria.

Saleh, A.A. (2012). Kwatanta Gamayyar Tasarifi da Tsarin Sautin Hausa da na Bade. Sashen Koyar da Harsunan Nigeria, Jami`ar Bayero, Kano.

Sulaiman, A.G. (2010). A Contrastive Analysis of Word Formation in Ebira and English Languages. MA Thesis Department of English and Literary Studies, Ahmadu Bello University , Zaria.

Temple, O. (1922). Notes on The Tribes, Provinces, Emirates and States of the Northern Nigeria, London, Frank Cass & Co LTD.

Tomori, S.H.O. (1977) The Morphology and Sytax of Present Day English: An Introduction, London, Heinmann.

Tsoho, D.M. (2006). Tuller Mission To Kamuku Land. Mustapha Printers SW Igbo Road, Off Lagos Road Streat, Niger State,Minna, Nigeria.

Waya, Z.I. (1997). Neuter Gender Formation in Hausa. Kundin Digiri na Farko, Jami'ar Bayero, Kano.

Wurma, A.G. (2005). Daidaitacciyar Hausa Da Qa'idojin Rubuta Ta, Kaduna: Olatunde Rasheed Publishers.

Yakasai, H.M. (2006). Hausa Reduplication in the Process of Grammaticalisation and Lexicalisation. PhD Thesis, Poland, Institute of Oriental Studies, Warsaw University.

Yule, G. (1996). The Study of Language, (second edition), Louisiana State University. Cambridge University Press.


Yusuf, O. (2010) Basic Linguistics for Nigerian Languages. Shebiotimo Publications, 72 Ararumi Street, Ijebu-Ode, Nigeria.

Yusuf, (2011). Kamanni da Bambancin Tasarifin Hausa da Larabci Kundin Digiri na Biyu Jami'ar Bayero, Kano.

'Yar'duwa, T.M. (1982). Quantifiers in Hausa. Kundin Digiri Na Biyu. Sashen Harsunan Nijeriya Da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria

Zarruq, R.M. (1999) Motsa kalma daga tilo zuwa jam'i. Takarda da aka gabatar a taron qara wa juna sani, Sashen Nazarin Harsunaan Nijerya, Jami'ar Bayero, Kano.

TASWIRAR YANKUNAN HARSUNAN NIJERIYA



TASWIRAR YAKUNAN KAMUKU

